JAMAHURIYAR NIJAR

MINISTAN GIDAN GONA

ƘUNGIYAR ƘASAR JAPON
MAI KULA DA HULƊ DA
ƘASASHEN DUNIYA
(JICA)

PROJEN MAI KULA DA BUNƘASA AYUKKAN NOMA A CIKIN FADANMU DA KE CIKIN YANKIN SAHEL A JAMAHURIYAR NIJAR (EDOS).

# LITTAHIN MALAMI

Ma'aikatar ƙasar Japon mai kula da bincike-bincike kan sha'anin kimiyar noma a cikin duniya (JIRCAS).

2008

# MAHAWARA

LITTAHIN MALAMI

MAHAWARA TA 1: Tashi da kanka

Al'ummar karkara musamman na fuskantar matsaloli iri-iri saboda haka aka hango ya dace a kafa ƙungiyoyi waɗanda ke ƙumshe da mutane masu sana'o'i kala-kala. Sai dai mafi yawansu suna mutuwa ne da puroje ko ƙungiyoyi masu zaman kansu sun janye hannuwansu. Wannan shi ya kawo dole a ba ra'ayin "tashi da kanka" ƙarhi wanda zai dogara da abinda al'umma ke mallaka wajen shahe ma kanta hawayenta kahin a nemi duk wani taimako daga waje. Don haka ne al'umma ya kamata :

- Ta haɗa kanta jama'a su zama tsintsiya maɗaurin guda saboda sarkin yawa ya hi sarkin ƙarhi.
- A bi lokacin da zamani ya kawo.

Tashi da kanka, wata husa'a ce mai ba mutane masu matsala iri ɗaya da su gano minene mafarin matsalarsu. Daga baya sai su tsara ayukka kuma su zartar da su da ƙarhinsu na jiki da kuɗinsu kuma tare da ɗaukar nauyin cin galaba ko na rishin nasara.

## Ma'anar ƙungiya ko koperatib da amfaninta

Ƙungiya ko koperatib ta karkara na ƙumshe ne da mutane masu sana'a iri guda, waɗanda ke fuskantar matsala iri ɗaya da suka amince su haɗu don su cimma manufa guda tare da yin aiki da demokaraɗiya a cikin tahiyar da aikinta. Jarin farko na ƙungiya yana samuwa ta hanyar haɗa hannuwa jari na mambobin ƙungiya daidai wa daidai. Dukan mambobi na ba da ƙoƙarinsu wajen zartar da ayukkan ƙungiya don haka ana raba daɗi da ciyyo tare.

Babbar aƙidar kowace irin ƙungiya shine :

- Haɗuwar jama'a
- Matsalolin da ake fuskanta iri ɗaya ne
- Niyyar bada kai ga duk kowane mamba wajen a gudanar da ayukkan ƙungiya ko koperatib
- Ra' ayin sana'a na kowa ne
- Ra'ayin kowa da kowa duk ɗaya a wajen ƙungiya.

Ƙungiya ta karkara tsari ne da ya dogara da haɗuwar jama'a in da za a bada ƙarfi ga :

- Ci-gaban mambobi da kansu
- Taimakon juna
- Idan daɗi ya samu kowa da kowa ya ji shi ba tare da fifiko ba
- Aiki da gaskiya a cikin tahiyar da ayukkan ƙungiya
- Yanci wajen yin duk wani aiki da ɗaukar nauyin jama'a.

Ba a kafa ƙungiya don gurin :

- Siyasa
- Addini
- Kabilanci

Ƙungiyoyi su ma zaman kansu suke, mallakar mambobinsu ne. Amma suna bin dokoki da ka'idodin ƙasa.

Ƙungiya na da manufar ba mambobinta muƙammai don su tahiyar mata da ayukkannta don ci-gaban kowa da kowa. Tana son cimma gurin :

- A haɗa ƙarfi da cikas-cikas na kowa da kowa,
- A ƙara arzikin mambobi ta hanyar ƙirƙiro ko ƙara kyautata ayukkan tattalin arzikinsu, ayukkan samo kayan aikin gona, ayukkan saye da saida kayan gona, ayukkan tattalin wuraren da aka tare ruwa da sauransu don ƙara jin daɗin rayuwarsu,
- Girkawa da ƙarfafa taimakon juna,
- ƙafa wasu ƙananan ƙungiyoyi don cudanya da wasu ƙungiyoyin horo da bada labaru.

## Mahawara bisa "Tashi da kanka"

Guri: Ɗalibbai su gane da abinda ake nuhi da "Tashi da kanka", ma'anar ƙungiya ko koperatib da kuma irin amfaninta.

Kayan aiki: misali na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mine ne ma'anar "Tashi da kanka" ? | -Husa'a ce mai ba mutane masu matsaloli iri ɗaya damar su tahi su gano ƙarhinsu su magance waɗannan matsaloli. |
| 2. Mine ne ma'anar ƙungiya koperatib? | -Haɗuwa ce ta mutane masu sana'a iri ɗaya kuma masu matsaloli iri ɗaya. |
| 3. Mine ne amfani ƙungiya ? | -Taimakon juna<br>-Ci-gaban mambobi<br>-Haɗa ƙarhi don biyan buƙatun juna |
| 4. Waɗanne irin ra'ayi aka hana sanyawa a cikin tahiyar da ayukkan ƙungiya ? | -Na siyasa<br>-Addini<br>-kabilanci |
| 5. Wa ke mallakar ƙungiyoyi ko koperatib? | -Ƙungiyoyi zaman kansu suke, mambobinsu ke mallakarsu amma suna bin dokoki da ka'idodin ƙasa |
| 6. Taƙaitacewa da jan hankali | |

MAHAWARA TA 2 : Babban taron ƙungiya

Ƙungiyar masu amfani da wuraren da aka tare ruwan gandari na tsare kamar haka :

- Ƙungiyoyi
- Babban taron ƙungiya ko majalisa
- Babban biro na zartar da ayukka
- Masu bincike
- Sashe-sashe iri-iri

### ➢ Babban taro

Ya hi komi mahammanci a ciki ƙungiya, yana ƙoli ga komi yana ƙumshe da duk mutane ko wasu ma'aikatu da suka yarda suka haɗa kansu don su haɗa ƙarhinsu wuri ɗaya don su cimma manufa guda.

Aikin babban taro shine :

- Ƙayyade manufa cikin gajere, matsakaici ko dagon lokaci dangance da duk abin da ya shahi ci-gaban karkara.
- Amince ma dokoki da ka'idodin ƙungiya ko gyaran fuskarsu.
- Babban zaɓen mambobi babban biro
- Zaɓen masu bincike
- Sanya mambobin sashe-sashe iri-iri.
- Amincewa wajen shiga wata ƙungiya
- Amincewa ma shiga ko hita duk wani mamba (gari ko zango)
- Ba biron zartar da ayukka izinin aikata ayukka da sunanshi.
- Roshe duk wasu tsare-tsare ko reshe na kungiya.

Duk kowane babban taro na da ka'idodi kamar haka :

- Cikakken yanci, matakkan da aka tsaida sun shahi kowa ba bambanci.
- Matakkan kiran taro, tsari, yanke magana da zance mafi yawan jama'a masu bada izinin a yi taro, ka'idodi da dokokin ƙungiya sun tsaida
- Zaɓen da duk da za a yi a yi aiki da demokarasiya a cikinshi
- Ana iya taro ƙayyadadde ko na musamman.

## Mahawara bisa babban taron ƙungiya

Guri: Ɗalibbai su gane da abinda ake nuhi da babban taro, ma'anarshi a cikin ƙungiya da kamar amfaninshi.

Kayan aiki: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1. Mi ake nuhi da babban taron ƙungiya ? | -Taro ne in da duka mambobi ƙungiya ke hallara.<br>- Aji ne na ƙoli na ƙungiya |
| 2. Wane lokaci ake yin shi ? | Ana yin shi a lokuttan da ake ƙayyade ko kuma tana kamawa musamman a yi shi. |
| 3. Wa ke shigabanci babban taro ? | Shigababn ƙungiya ko mataimaikinshi ko magatakarda |
| 4. Wane irin nauyi ke rataye a wuyan babban taro ? | - ƙayyade manufofi<br>- Zaɓen mambobin biron zartarssuwa<br>- Sa yan bincike<br>- Kulla da hulda da wasu ƙungiyoyi<br>- Roshe duk wasu tsare-tsare ko reshe na kungiya |
| 5. Taƙaitacewa da jan hankali | |

## Mahawara ta 3

### Biro mai zartarwa

Babban taro ke haihuwarshi kuma shi ke rataya mashi nauyin zartar da ayukkan ƙungiya na yau da kulllum. Mambobin biron zartarsuwa, naɗa su babban taro ke yi kuma ba wanda ya hi wani don haka in aiki yayi kyau kowa ne idan bai yi ba kuma duka kowa na da laihi. Aikinshi shine :

- Tsarawa da tahiyar da ayukkan rayawa da bunƙasa ƙungiya
- Bi sau da ƙafa, tsarawa da zartar da tsarurruka na ƙungiya
- Saka ma sassa wasu daga cikin ayukkanshi
- Bi sau da ƙafa wasu ayukkan da aka tsara
- Tahiyar da ayukkan awon ayukkan na kanka da kanka
- Shirin taronni
- Wakiltar ƙungiya zuwa wajen wasu ƙungiyoyi, masu hannun da shuni ko wajen sharï'a
- Bada bayanai a rubuce na ayukkan da aka yi a wata- wata ko kuma karshen shekara.

Aikin biron zartarwa ba ya da biya. Amma duka wasu kashe-kashe da suka shahi tahiyar da aiki ana biyan su, biro mai zartarwa yana aiki ko da yaushe ne don haka ne ƙungiya ta cancanta a ce tana da mazamni, ana nuhin biro ko ma'aikata ko kuma lambar waya

Biro mai zartarwa shi ne ke da nauyin tabattar da aiki na tahiya daidai. Shi ke zartar da ayukkan da babban taro ya damƙa mashi. Ana zaɓen mambobin biron zartarwa a tsawon shekaru 3 kuma ana iya sake zaɓensu.

Doka ba ta tsaida ba sau nawa ake iya sake zaɓen mambobin biron zartarwa suna, kenan ana iya sake zaɓensu ko sau nawa ake so.

Matakkan da biron zartarwa suna aiki lokacin da mafi yawan mambobi suka amince masu idan aka samu tangam na kuri'a ra'ayin shigaba shike ci.

Biron zartarwa na taruwa lokaci-lokaci amma mambobi ke tsaida yawan taronnin da za su yi da kuma lokuttan da ya dace a riƙa haɗuwa.

## Mahawara bisa biron zartassuwa

Guri: Ɗalibbai su gane da abinda ake nuhi da biron zartarwa, aikinshi da amfaninshi cikin ƙungiya.

Kayan aiki: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mi ake nuhi da biron zartassuwa ? | -Biro ne na ƙungiya mai tahiyar da ayukkan ƙungiya da sunanta yana ƙumshe da mambobi da babban taro ya amince ma |
| 2. Wa'adi nawa mambobin biron zartassuwa ke iya yi ? | Wa'adin shekara 3 amma ana iya zaɓen su daga nan ko da yaushe sai ma sha allahu in suna tahiyar da ayukkansu da kyau. |
| 3. Mine ne ayukkan biron zartassuwa ? | Tsara taronnin babban taro<br>Zartar da matakkan da babban taro ya tsaida<br>Wakiltar ƙungiya a ko'i na |
| 4. Taƙaitacewa da jan hankali | |

## Mahawara ta 4 : Yan bincike

Masu bincike a cikin ƙungiya tamkar babban taro ne a kusan biro mai zartarwa da aka zaɓa don tahiyar da ayukkan ƙungiya. Masu bincike sune idanuwan ƙungiya wajen kulawa da kididdigar dukiya ƙungiya.

Nauyi da wa'adin mambobin masu bincike an ambato su cikin kundayen ƙungiya kamar dokoki da ka'idodin ƙungiya. Ayukkan masu bincike sune la'akari da bincike saboda a tabbatar da lahiyar da kwanciyar hankali da yarda tsakanin juna da kuma a cikin ƙungiya gaba ɗaya.

Don haka babban taro, tilas ne ya naɗa mutum 3 masu bincike waɗanda aikinsu bincike ne duka lokacin da suka ga dama.

Bincike don tabbatarwa da lalle biron zartarwa na aiki da matakkan da babban taro ya tsaida :

- Binciken shiga da hutar kuɗi,
- Girgam,
- Dukiyar ƙungiya (ginoni da sauran kadarori),
- Bincikawa don gano ingancin bayanai na rubuce da biron zartarwa ke yi ma ƙungiya.

Masu bincike na gabatar da rohoton ayukkan da suka yi a wajen babban taro dangance da nauyin da ya ɗora masu. A cikin kundayen ƙungiya an riga an zana aikinsu dalla-dalla. Ba su da albashi in mambobin ƙungiya ne.

## Mahawara bisa yan bincike

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mine ne ma'anar masu bincike ? | Mutane 3 ne masu binciken dukiyar ƙungiya da sunanta |
| 2. Wa ke naɗa su ? | Babban taron ƙungiya ke naɗasu kuma ya rataya masu nauyi. |
| 3. Ina su ke bada labarin aikin da suka yi ? | A gaban babban taro na ƙungiya |
| 4. Wane lokaci suke yin bincikensu? | Ba su da lokaci kuma suna binciken asusu ko kadarori. |
| 5. Masu bincike har suna da albashi? | A'a in mambobin ƙungiya ne. |
| 6. Taƙaitacewa da jan hankali | |

**Mahawara ta 5**: sassan ƙungiya, zaɓen wakkillai

a) **Sassan ƙungiya**

Idan buƙata ta kama, ƙungiya na iya kafa sassa don su kula da wasu ƙayyadaddin ayukkan ƙungiya. A ka'idance babban taro na ƙungiya ke kafa su saboda a ƙarƙashinshi suke. Amma suna aiki ƙarƙashin biron zartarwa. Nauyi da ke wuyansu da yadda suke tahiyar da ayukkansu an ambato su dalla-dalla a cikin kundayen ƙungiya.

b) **Zaɓen wakillai**

Kahin a shiga takara wani muƙami a cikin ƙungiya sai mamba ya cika ka'idodi kamar haka:

- Ya zamanto mutun ba ya tsare a gidan kaso (yari),
- Sai in mutun ya amince kuma ya yarda da aikin sa kai,
- Sai mutun ƙwararre da jama'a ta tabbatar da haka,
- Sai mutun wanda ya iya bada bayani kuma ya iya bada labari,
- Sai mai ƙoƙari kuma mai dama ko da yaushe,
- Sai mai husa'a,
- Sai mutun wanda ya iya karatu ko na turanci ko da halsunan gida, yana da kyau in ya samu.

## Mahawara bisa sassan ƙungiya da zaɓen wakillai

**Guri**: Ɗalibbai su gane ma'anar sassan ƙungiya da kuma yadda ake zaɓen wakillai.

**Kayan aiki**: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mi ake nuhi da sassan ƙungiya ? | -Kwamitoci ne da ƙungiya ke sa wa don su gudanar da mata da wasu ayukkan na masamman. |
| 2. A ƙarƙashin wa suke aiki ? | Suna aikinsu a ƙarƙashin biron zartassuwa na ƙungiya. |
| 3. Waɗanne irin ka'idodi mutum ya kamata ya cika kahin a zaɓe shi wakili ? | Wanda ba ya kaso<br>Wanda ya yarda<br>Kwararre cikin aiki<br>Mai bada labari da bayani<br>Mai ƙoƙari da husa'a<br>Wanda ya ima kanshi<br>Wanda ya san karatu |
| 4. Taƙaitacewa da jan hankali | |

## Mahawara ta 6 : Odar kayan noma

Galubi ƙananan manoma na fuskantar matsala wajen mallakar kayan noma na kirki (taki, iri da magani) wanda za su daɗewa ana yi. Bayan haka kayan gona parashinsu saurin sakewa yake yi tsakanin lokacin kaka da na bazara.

Tsakanin kaka da bazara. Amma duk da haka manomi na banzata kayan gonarshi don ya biya wasu buƙatunshi. Bayan haka saboda ba inda zai je dole ya faɗa hannuwan miyagun yan kasuwa sai su saida mashi kayan gona mars kyau kuma a makare. Don magance waɗannan matsaloli ya dace da a ƙafa kantuna na saida kayan gona in da manoma suke tayihar da saide-saide da kansu don kansu. Kantin saida kayan gona na kyautata samun kayan gona ta hanyar :

- Saida kayan gona ƙwara-ƙwara
- Hada ƙarhi wajen yin odar kaya
- Hayar ƙananan kayan gona
- Kashe ƙwari tare da birgadiye
- Yaɗa kayan gona da yaɗa sabin husa'o'in noma
- Bunƙasa yin maganin dabbobi tare da haɗin gwiwar likitocin dabbobi
- Nomawa da saida iri na zamani
- Horo da bada lobari bisa yadda ake iya amfani da kayan gona.

Amma kantin kayan gona in a na so aikinshi ya yi kyau sosai sai waɗannan ka'idodi sun cika :

- Sai an sami masu buƙata masu yawa,
- Sai an sami al'umma wadda ta ɗauki alkawalin gina wurin sa kaya da kuma kawo gudumuwarsu wajen jarin farko,
- Samun mutanen da suka iya karatun yaƙi da jahilci ko na lokkwal don su riƙe muƙamin masu saidawa,
- Samun mangaza mai buɗawa kullum a lokacin da kowa ya sani,
- Saidawa kuɗi hannu,
- Kantin ya ƙumshi kaya iri-iri da ake saidawa kuma ba su katsewa,
- A ja hankali da bada labari ga al'umma da ke kewaye da wajen.

Ana kafa kwamiti mai kula da odan kaya, saida kaya da kuma tahiyar da duk ayukkan kanti lokaci zuwa lokaci ya kamata yana ba al'umma bayani. Kwamiti na bunƙasa ayukkan kanti ta hanyar neman labari na parashin kaya saboda ya riƙa odar kayan yadda kullum in aka buƙata a sayo, in an saida a ci riba kuma cikin an yi ma manoma sauƙi.

## Mahawara bisa unfanin kafa kantin kayan noma

Guri: Ɗalibbai su gane yadda ake odan kayan noma kuma su gano amfani saida su a cikin kanti kayan gona.

<u>Kayan aiki</u>: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mi ake nuhi da odan kayan gona ? | -Sayo kaya kamar su iri, taki da magani don a riƙa saida manoma masu ƙaramin ƙarhi. |
| 2. A ina ake saida kayan noma ? | A cikin kanti na kayan noma na gari |
| 3. kantin kayan gona mallaka wa ce ? | Al'ummar gari ko koperatb da ta kafa kantin ita ke da shi kuma ita ke haɗa jalli kafashi. |
| 4. Mine ne amfani kanti kayan gona? | Samun kayan gona masu sauƙi masu kusa ga gida a duk lokacin da ake so<br>Maganin yaudarar manyan yan kasuwa |
| 5. Wa ke iya saida kaya a cikin kanti | Sai adili wanda ya iya karatu da rubutu. |
| 6. Taƙaitacewa da jan hankali | |

## Mahawara ta 7 : kyautata sanin al'umma bisa ga kiwon lahiya da tsabta

Saboda kyautata lahiyar mutane an gudanar da ayukkan rigakahi da na yi ma al'umma magani ma. Ana iya zana tsabtace miyagun ruwa don su zama ruwa na sha na kirki da kuma ɗaukar mattakai na yaƙi da zazzaɓin cizon sabro. Abinda ya shahi zazzaɓin cizon sabro, sabro shine mafari masassara wadda ta dami mafi yawan al'umma, ya kamata :

- A kashe ramu masu kwantar da ruwa,
- A ruhe ramu masu hidda lalakun ruwa,
- A ruhe kwankuna ko leda in da sabro ke iya rayuwa,
- A nome ciyawa da ke cikin gidaje da kewayensu,
- A ƙone ƙazamta can nesa ga gari,
- A riƙa ruhe wuraren sa ruwa,
- A riƙa kwana cikin gidan sabro wanda aka sanya ma magani,
- Sanya tufafi masu magani ɗari da marace,
- Mata masu juna biyu su riƙa rigakahi masassara cizon sabro duk tsawon lokacin da suke da ciki don su kare kansu da ɗansu.

### a) tace ruwan sha

Idan ana son tace ruwa sai a ɗaura ƙyalle mai tsabta a bakin randa ko bokiti a zuba ruwa saman ƙyallen. Ana iya amfani da dubarar tace ruwa ta hanyar yin kwanci-kwanci na ƙasa, tsakuwa da gawai. Sai a yi kwanci-kwancinsu cikin tukunya ko bokiti ko ƙwarya amma masu hudodi ƙasa yadda duk wata ƙwayar cuta ba za ta iya wucewa ba.

Ga yadda kwanci-kwanci suke : kwanci na farko, yan manya-manyan duwatsu da duwatsu madaidaita, kwanci na biyu yan ƙananan duwatsu, kwanci na ukku ƙasa (rairai), kwanci na huɗu gawai ne, sa'annan sai a zuba ruwa amma kar a manta a wanke yan duwatsuna da gawai da kyau kahin a sanya su a cikin tukunya ko bokiti ko ƙwarya mai huduna.

### b) Dahuwa ruwa

A dafa ruwa a ƙalla tsawon minti 30. Dafa ruwa na sa duka miyagun ƙwayoyin cuta su mutu kap sa'annan sai a sami ruwa tsabtacce na sha.

### Mahawara kan kyautata sanin al'umma bisa ga kiwon lahiya da tsabta

Guri: Ɗalibbai su kyautata saninsu wajen kiwon lahiyarsu da tsabtarsu.

<u>Kayan aiki</u>: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1. Mi ake nuhi da kiwon lahiya al'umma ? | Ayukkan ne da suka shahi riga kahi na lahiyar jama'a. |
| 2. Ku zana ayukkan da suka shahi kiwon lahiya ? | - Tsabtace mahalli (ruhe ramu in da ruwa ke kwanci, ƙone kwankuna, noma ciyawa a cikin gidaje da sauransu)<br>- Tace ruwa na sha<br>Dafa ruwa. |
| 3. Mine ne amfanin tsabtace mahalli da ruwan sha? | Kariya ga masassara cizon sabro da sauran cututtuka da ake iya ɗauka cikin ruwan sha da a cikin iska gurbatacce. |
| 4. Taƙaiewa da jan hankalin malami | |

## Mahawara ta 8 : Mallakar ƙasa a cikin kwanciyar hankali

Idan ana son a daɗe ana cin moriyar wurin noma to sai an tabbata da an mallaki wuri. Dan haka ne aka kafa ƙungiyar gari mai kula da sha'anin bada shaida ta mallakar ƙasa. Wannan ƙungiya ana kafa ta tare da haɗin gwiwar ma'aikatun gwamnati, hukuma, sarakkan galgajiya da manoma da makiyaya. Aikinta shine :

- Kiyaye rikicin ƙasar noma,
- Taimaka ma hakimi wajen cika takardar rahoton shirin rikitta,
- Shiga gaba wajen hidda wuraren burtulla, wuraren makiyaya, wuraren mashaya da wuraren hutawar bisashe,
- Bada labari da jan hankalin al'umma dangance da dokar kasa da ta shahi karkara,
- Taimaka hakimi wajen bada takardun shaida,
- A tsaya a faɗi dalla-dalla irin ma'amalar da ke tsakanin ƙungiyar ƙaramar hukuma ko kuma ƙungiyar gunduma.

Ƙungiyar gari na bada takardar shaida iri biyu :

a) **Takardar shaida ta dindindin:**

- Takardar shaidar mallakar wurin a galgajiyance;
- Takardar shaidar saida wurin ;
- Takardar shaidar bada wurin ;

b) **Takardun shaida waɗanda ba na dindindin ba :**

- Takardar shaidar jingina ;
- Takardar shaidar haya ko suhuri ;
- Takardar shaidar bada aro.

Ga hanyoyi neman kowace takarda wajen ƙungiyar gari :

- Tambayar takarda a rubuce ko a baki a wajen shigaban ƙungiya mai kula da bada waɗannan takardu;
- Nazarin tambayar;
- Gabatar da masu shaidu a gaban mambobin ƙungiya;
- Bayanai na tabbatar da gaskiyar yin takardar;
- Maga takarda ya cika takardar;
- Sa hannun masu shaidu da maƙwabta;
- Sa hannun hakimi shigaban ƙungiya;
- A ba wanda aka yi ma takarda kopi guda ƙungiya ta riƙe kopi guda.

**Mahawara bisa mallakar ƙasa a cikin kwanciyar hankali**

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1. Mi ake nuhi da ƙungiyar gari mai bada shaidar mallakar mallakar wari ? | Ƙungiya ce wadda doka ta ƙasa ta amince don ta magance rikkita na wurare |
| 2. Wa ke shugabancin ta ? | Hakimi na gari ko rugga ko na zango |
| 3. Mine ayukkanta ? | Kiyaye rikitta, hidda wuraren shan ruwa na bisashe, burtali, makyaya da sauransu. |
| 4. Takardu kala nawa ne ƙungiya take badawa ? | Kala biyu ne :<br><br>1. Akwai na dindindin :<br><br>- takardar mallakar wuri a galgajiyance;<br>- ta shaidar sayen wuri;<br>- ta shaidar bada wuri kyauta.<br><br>2. Akwai waɗanda ba na dindim ba :<br><br>- takardar shaidar jingina;<br>- ta shaidar haya;<br>- ta shaidar bada aro. |
| 5. Taƙaitawa da jan hankalin malami. | |

## <u>Mahawara ta 9</u> : Tsarin cin moriyar gandari

Tsarin cin moriyar gandari, tsari ne na tada jama'a na haɗa kan jama'a na haɗa ƙarhi da kayan aiki na jama'a masu amfani da gandari don yin wasu ayukka saboda hana ma wasu ma tsaloli haɓaka kuma a samu a ci amfani gandari yadda ya kamata. Ana iya samun matsaloli bisa gandari masu wuyar magancewa a gaugauce. Tsarin cin moriyar gandari tsari ne wanda ke bada damar a yi tsari na dubaru, na kayan aiki, na mutane da na kuɗaɗen da suka isa don a ciyo kan matsaloli. A taƙaice don a kawo haske ne bisa abinda za a aikatawa kuma da mi za a aikata shi da kuma ƙaƙa za a aikatawa, wane lokaci kuma wane lokaci zai ɗauka. Yana bada damar a auna ga in da aka tashi kuma ga in da ake fatar zuwa na alheri.

Tsarin cin moriyar gandari tsarin shekara ne kuma ya ƙumshi :

- Duka ayukkan da za a yi a tsawon shekara,
- Duka wuraren da kuɗaɗden za su hito,
- Lokacin da za a gudanar da ayukka,
- Waɗanda za su yi ayukkan da kuma waɗanda za su bi ayukan sau da ƙafa.

Duka ayukkan da za a rubuta a cikin tsarin cin moriyar gandari na shekara sun shahi matsaloli da manoma ke fuskanta ne a bisa gandari. Waɗannan ayukka ana yin kuɗaɗe kamar haka :

- Zuba-zuba na masu aiki bisa gandari da babban taro ke tsaidawa
- Tarbace da ake yi idan za a yi wani aiki na cikin tsarin cin moriyar gandari
- Taimakon mambobi ko kuma wani mutum ko ma'aikata mai son ayukkan gandari
- Tara da aka yi ma wasu yan ƙungiya da suka yi laihi da babban taro ke yanke adadin kuɗin tara
- Kudaɗe masu shigowa musamman da izinin shugabani kamar su gudumuwa, tahiyar da manyan taronni da wasu wasanni da aka yi da sunan ƙungiya.
- Wasu husa'o'i masu kawo kuɗi sawo na riba ƙungiya bayan an yi kasuwanci ko kuma ribar da ta shigo ta hanyar bada basussuka.

## <u>Mahawara bisa tsarin cin moriyar gandari</u>

<u>Guri</u>: Ɗalibbai su gane amfani da mahimmanci yin tsari cin moriyar gandari na shekara-shekara.

<u>Kayan aiki</u>: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mi ake nuhi da tsarin cin moriyar gandari? | -Tsarin ne na shekara-shekara da manoman gandari ke yi don magance matsalolinsu. |
| 2. Wa ke yi musu wannan tsari ? | Su manoma sukeyi ma kansu tsari. |
| 3. Wake basu kuɗi su yi ayukka ? | Zuba-zuba na manoma masu amfani da gandari<br>Tarbace<br>Taimako ko gudumuwar wasu masu hannu da shuni. |
| 4. Taƙaitacewa da jan hankali | |

# Mahawara ta 10 : Taimakon wuraren noma da taki

Taki taimako ne ga ƙasar noma da abubuwan da shibke-shibke ke buƙata don su yi rayuwa mai kyau. Taki ya kasu kashi biyu, akwai na galgajiya (kashin bisashe da karmami) kuma akwai na zamani. Amfanin takin galgajiya shine :

- Bunƙasa sayyun shibke- shibke,
- Sanya ƙasa ta yi ƙarhi,
- Rage zaizzayewa ƙasa,
- Ƙara ma ƙasa ƙarfin riƙe ruwa,
- Bunƙasa wasu sinadarorin da ke cikin ƙasa.

Ana sa takin galgajiya kahin a fara gyran gona ana kai taki mangala- mangala a cikin gona sai a sa hannuwa a watse shi ana watse taki lokacin da za a fara noma saboda kar a yi hasara wasu abubuwar da ke cikin taki masu mahimmanci (azot). Takin galgajiya na da amfani ƙwarai wajen gyaran ƙasa. Idan ana son wuri ya ji taki ko da yaushe sai an riƙa kai tan 5 zuwa 10 duk shekara na takin da ya ruɓa ko a sa ya ruɓa.

Abinda ya shahi takin zamani, ga yadda ake sanya shi cikin shibke-shibke kamar su hatsi, dawa da sauransu :

- A wwatsa takin zamani fosfate kahin a yi shibka bai ɗaya a cikin gona sai a bi shi da noma na ƙeƙashe, misali kg 100 na ssp kowace eka da kg 5 na stp kowace eka.
- A sanya takin zamani a lokacin shibka, takin sai a sa shi cikin ramu sa'annan a sanya iri sai a ruhe rame. Adadin shine kg 20 eka 1 kenan g 2 kowane rame na takin zamani DAP ko kg 60 eka kenan g 6 kowane rame in takin zamani 15-15-15 ne.
- Wajen noma rani sanya taki yana dangance ne da irin kowace shibka. Don haka yana da mahimmanci a tuntuɓi malaman gona.

Mahawara bisa taimakon wuraren noma da taki

Guri: Ɗalibbai su gane mahimmanci taimaka ma wuraren noma da taki da kuma yadda ake sa shi.

Kayan aiki: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mi ake nuhi da taimaka ma wuraren noma da taki ? | Kai taki a gonaki<br>sa takin zamani ga wuraren noma. |
| 2. Yaya ake sanya taki acikin gonaki ? | Ana sanya na zamani kahin a soma gyaran gona sai a juya ƙasa<br>Ana sanya rami-rami lokacin shibka<br>In na galgajiya ne ana watse shi lokacin ana noma. |
| 3. mine ne amfani taki ga ƙasar noma ? | Yana sa ƙasa ta yi ƙwari, ta yi ƙyau, ta saki duka sinadaranta masu amfanin shibke-shibke. |
| 4. Taƙaicewa da jan hankali | |

## Mahawara ta 11: noman rani

Noman rani sana'a ce mai taimakawa wajen bunƙasawa da yawanta arzikin manoma. Idan manomi na son yin noman rani sai ya yi :

1. aiki da yanayin karkara da zai yi noman rani a cikin zaɓe shibke-shibken da zai nomawa ; Misali :

- *ga lokacin sanyi* ( nobamba, janairu, fabarairu) duka irin shibke-shibke ana iya noma su ;
- *Ga lokacin zahi* (maris, zuwa mayu) noman rani wuya gare shi. Shibke-shibke waɗanda suka hi dacewa sune : guna, malo, kwankwanbir, tibis da kuɓewa ;
- *Ga lokacin damana*, shibke-shibke da suka hi dacewa sune tumatir (icri xina) tanka (hot habanero da safi) attarugu (super beitar) (yolo wonder da gandisimo) salati (maya) da kuɓewa.

2. Mallakar wuri na noma da ya dace da irin shibkar da aka zaɓa,
3. Tabbatawa da akwai isassun ruwan bai a wuri kuma da za a amfani da su yadda ya kamata,
4. Zaɓen irin shibke-shibke dangance da dacewarsu ga wuri, da tsawon lokaci kahin su kai, da irin albarka da ake iya samu, da rashin matsalar sarrafa su da ajiyarsu da saurin saidawa da amfani da ake iya samu da kuma tsarin nomansu da irin husa'o'in da za a yi amfani da su wajen noman irin waɗannan shibke-shibke,
5. A bi ka'idodin noman irin shibkar da aka zaɓa: renon irin dashe, tattalin shibka (ɗan maimai, sa taki da sa magani).

Idan manomi na son ya sami albarkar noma sosai to ya riƙa neman gargaɗin malaman gona.

Mahawara bisa : noman rani

Guri: Ɗalibbai su gane ka'idodin noman rani da kuma lokuttan da suka dace wajen noman rani.

Kayan aiki: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1.Mi ake nuhi da noman rani? | Noma da ake yi bayan an ƙare na damana a cikin fadɗammu ko a cikin kware. |
| 2. Waɗanne ka'idodi mai noman rani ya kamata ya cika ? | Aiki da yanayin karkara<br>Mallakar wurin noma<br>Tabbatawa da akwai isassun ruwan bai<br>Zaɓen shibke-shibke waɗanda suka dace<br>Bin ka'idodi dalla-dalla tun renon iri sai shibka ta kai. |
| 3. Wane lokaci ne duka shibke-shibke suka hi yi ? | Ga lokacin ɗari (nobamba zuwa fabarairu) |
| 4. Wace shawara manomi ya kamata ya yi aiki da ita idan yana son amfani mai yawa? | Malaman gidan gona ko wani masani kimiya aikin noman rani |
| 5. Taƙaicewa da jan hankali | |

## Mahawara ta 12 : Tattalin gandari ko baraji

Saboda a jima ana cin moriyar gandari ko baraji sai an kafa tsarin tattalin gandari (ƙananan baraji da dam). Tsarin zai sa a tsara ayukkan tattali da na rigakahi ta hanya amfani da kaɗannin kayan aiki don tsari ya tahi da kyua , ya dace a sa ƙungiya mai kula musamman da tattalin baraji wadda za ta rungume duka ayukkan tattali. Ayukkan wannan ƙungiya sune :

- dubawa ta yau da kullum (ziyara dubawa),
- tsara tsarin cin moriyar gandari na shekara
- jan hankali manoma don su bada ƙarhi wajen tattalin gandari,
- sa manoma su bada mutane, kuɗi da kayan aiki isassu don yin ayukkan tattali,
- ziyara duba gandari lokacin da ruwa suka zo.

Wannan nauyi ba ya buƙatar ƙwareya sosai. Don haka sai an sa natsuwa, kuzari da ƙoƙari kullum. Ƙungiya ko birigad mai kula da tattalin baraji ko gandari na da shugaba da mabobi. Don sauƙaƙa ayukka, shugaba da mambobi ana zaɓen su a cikin garuruwa mafi kusa ga gandari ko baraji.

Wannan ƙungiya za ta ayukkan da ba su wuce ƙarhinta ba ; sune :

**a) cike ramu**

- ƙarama yar gebeya girma don ta dan kama mai dorewa
- jera duwatsu bisa hanya ruwa
- cika yan gyabbu da kwaɓɓaɓen ɓurji
- kashe mafari gyabbu
- kare baraji ko gandari da kar ya zama hanyar bisashe

**b) Tattali na dutsi**

- A hidda duwatsun da ba su da kyua
- A kwaɓa ɓurji a cika in da ruwa ke gangarawa

**c) a hidda hakukuwa maras kyau**

Barin itatuwa da ciyawa kusan baraji da gandari na iya jawo matsaloli kamar haka :

- ɗagowar gandari in sayyu sun girma,
- ruwa na iya kwarar wurin da sayyu suke in icce ya mutu har ya kai baraji ya fashe.

Ga matakkan da ake ɗauka :

- A kashe duk wani icce da ke nisa meter 10 daga baraji,
- In an bar icce ya girma, sayyu girma suke yi sa'annan an hi matsala lokacin nan,
- In icce ya girma ƙwarai kar a hidda shi kwata kwata har ga sayyu don tofowa yake yi,
- Idan aka ƙare a maida duka kayan da aka yi aiki da su kar a yi sakaki.

**d) tattali na ɗarmun dutsi**

Idan ɗarmun dutsi bai lalace sai a warware shi a gyara in ya lalace sai a sa a yi sabin ɗarmu.

**e) kokowa da ambaliyan rairai**

Wasu gandura tun wurin yin su ana barin wurin da yake rage ruwa ko dauɗa. Amma idan an raya saman dabagi kuma aka yi mashi shibke-shibken itatuwa ya hi kamar su bankyet, rabin wata da ramun dasa itatuwa.

Idan ƙungiya ko birigad mai tattalin na son yin ayukka sai ta mallaki waɗannan kayayyaki :

- Helu
- Kwasa
- Bambara
- Dam na hannu
- Burweti
- Bokitinnai
- Tano yamti
- koshiyar gina
- addaye
- ratonni
- arozuwar
- tenayi
- painsi

Ga yada ƙungiya ya kamata ta yi tsarin aikinta :

- Ziyarce-ziyarce na yau da kullum don a gano da wuri mai matsaloli,
- Ziyara lokacin da ruwa suka zo don a dubi abubuwan awon ruwa,
- Ziyara bayan ruwa sun jaye don gani in babu ɓanna.

## Mahawara bisa : ga tattalin gandari ko baraji

Guri: Ɗalibbai su gane mahimmanci tattalin gandari da yadda ake yin ƙananan tattali.

Kayan aiki: misali ko kwatamce na baki

| Malami | Ɗalibbai |
|---|---|
| 1. Mi ake nuhi da tattalin baraji? | Ƙananan gyare-gyare da masu aiki bisa ga gandari ya dace su riƙa yi lokaci zuwa lokaci don a daɗe ana cin moriyar gandari. |
| 2. Wake jagoranci kulawa da gandari ? | Ƙungiya ko birigad da manoma suka wakilta ma zartar da duk wani aiki na gyaran gandari. |
| 3. wa ke ba ta kayan aiki ? | Manoma da ke aiki bisa gandari (zuba-zuba, tara da kyau da sauransu) |
| 4. Tsarin aikin ƙungiya da mi da mi ya ƙumsa ? | Ziyarce-ziyarce na yau da kullum<br>Ziyarca lokacin da ruwa suka zo<br>Ziyara bayan ruwa sun janye. |
| 5. Taƙaitacewa da jan hankali | |

# Karatu da rubutu

*Littahin malami*

## DARASI NA 1

1. **Aikin yau: koyon rubutun alamomi:**

Guri : Dalibbai su gane waɗannan alamomi kuma su iya rubuta su.

2. **Tahiyar da aiki :**

- malami ya faɗa ma dalibai mahimmancin waɗannan alamomi a cikin rubuce rubuce da za a yi nan gaba.
- malami ya rubuta alamomin gudu gudu bisa babban allo kuma ya tambaye su; kama da mi suke yi ?
- malami yi tambayi ɗalibbai su kwatanta sunan alamomi

Amsa:

| | |
|---|---|
| • | ɗigo |
| I | doguwar sanda a tsaye |
| – | ƙaramar sanda a kwance |
| / | ƙaramar sanda gilme a dama |
| \ | ƙaramar sanda gilme a hagum. |

- ya sa ɗalibbai su dubi alamomin sosai kuma su zana su bisa allunan su
- ya gayyaci mafi yawan ɗalibbai su rubuta alamomin bisa babban allo. Ya ci gyara.

# DARASI NA 2

## 1. Tilawa bisa alamomin baya

Malami ya tambayi ɗalibbai irin alamonin da suka gani baya :

• , I , / , - , \

## 2. Aikin yau:koyon rubutun alamomi

Malami ya rubuta alamomin guda-guda bisa babban allo kuma ya tambayi ɗalibbai kama dami suke yi ?

**Amsa :** C : alamar baka
Ɔ : alamar sabon wata
O : kurtu
ʃ : Makaɗi : juye
ɳ : Makaɗi gora
J : Mamar lema
S : Gujiya

- Ya sa ɗalibbai su dubi alamonin sosai kuma suyi zanen siffofinsu su bisa ƙananan allunan su ;
- ya gayyaci mafi yawan ɗalibbai su rubuta alamomin bisa babban allo.

# DARASI NA 3

1. **Tilawa bisa aikin baya**

Malami ya gayyaci ɗalibbai su rubuta wasu alamomi bisa allunan su

Ya duba sa'anan aci gyara bisa babban allo.

2. **Aikin yau: karatu da rubutuni da O**

Tahanyar hoto malami ya hiddo jimilar da za a aiki da ita.

## Kungiya na da amfani iri . iri.

Malami ya rubuta kalmar a babban allo : iri

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta

Ya sabko faɗar dake ƙumshe da wasalin da za a aiki da shi

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

Ya sabko wasalin ƙarƙashin faɗar

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta wasalin

ri

i

Ya rubuta wasalin da babban rubutu

Ya gayyaci ɗalibbai su je babban allo, su rubuta wasalin

Ya sa ɗalibbai su rubuta wasalin bisa allunan su

Ya duba domin cin .gyara a babban allo

Malami ya bi hanyar da ya bi wajen karantar da "i" domin ya karantar da "O"

Malami ya rubuta i da o a tsabbace a babban allo

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

| | | |
|---|---|---|
| i | i | i |

| | | |
|---|---|---|
| O | O | O |

Ya gayyaci ɗalibbai su ɗauki rubutun cikin kayyunan su ya gewaya domin cin gyara.

# <u>DARASI NA 4</u>

**1.Tilawa bisa aikin baya**

Malami yayi shibtar **i** da **o**

Ya gayyaci ɗalibbai a babban allo domin cin gyara.

Bayan cin gyara malami ya karanta kuma ya sa mafi yawan ɗalibbai su karanta.

**2. Aiki yau: karatu da rubutu a da u**

Ta hanyar hoto malami ya tambayi ɗalibbai abun da suke gani?

Amadu magatakarda ne

Malami ya rubuta kalmar a babban allo

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta

magatakarda

Ya sabko faɗar da ke ƙumshe da wasalin da za a aiki da shi ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

ga
a

Ya rubuta wasalin da babban rubutu

a a a

Ya gayyaci ɗalibbai su je babban allo su rubuta wasalin

Ya sa ɗalibbai su rubuta wasalin bisa allunan su

Ya duba domin cin gyara bisa babban allo

Malami ya bi hanyar da ya bi wajen karantar da **a** domin ya karantar da **u**.

Malami ya rubuta **a** da **u** a tsabace a babban allo ya karanta ya sa ɗalibbai su karanta.

| | | |
|---|---|---|
| a | a | a |

| | | |
|---|---|---|
| u | u | u |

Ya gayyaci dalibbai su ɗauki rubutu cikin kayyunan su ya gewaya domin cin gyara.

# DARASI NA 5

1. **Tilawa bisa aikin baya**

Malami ya ti shibtar **a** da **u**

Ya gayyaci ɗalibbai a babban allo domin cin gyara

Bayan cin gyara malami ya karanta kuma ya sa mafi yawan ɗalibbai su karanta.

2. **Aikin yau: karatu da rubutu e da ai da au**

Ta hanyar hoto a hito a hiddo jumilar da za a aiki da ita

Malami ya rubuta kalmar a babban allo

**helo**

Ya sabko fadar dake ƙumshe da wasalin da za a aiki da shi.

Ya karanta ,kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

**he**

Ya sabko wasalin ƙarƙashin faɗar

Ya karanta, kuma ya sa ɗalibbai su karanta wasalin

**he**

**e**

Ya rubuta wasalin da babban rubutu

| | | |
|---|---|---|
| e | e | e |

Ya gayyaci wasu daga cikin ɗalibbai su je babban allo su rubuta wasalin a ci gyara.

Ya sa ɗalibbai su rubuta wasalin bisa allunansu ya duba domin cin gyara.

Malami ya bi hanyar da bi wajen karantar da **e** domin ya karantar da **ai** da **au**.

Malami ya rubuta **e** de **ai** da **au** a tsabbace a babban allo ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

| | | |
|---|---|---|
| e | e | e |
| ai | ai | ai |
| au | au | au |

Ya gayyaci ɗalibbai su ɗauki rubutun cikin kayyunansu ya gewaya domin cin gyara.

# DARASI NA 6

**Babbar tilawa :** Malami ya yi shibtar duk aikin da ya yi baya

| | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|
| i | u | o | a | ai | au | e |

- A ci gyara bisa abban allo
- Malami y rubuta shibtar a tsabbace bisa babban allo.
- Ya gayyaci waɗansu ɗalibbai su karanta, shi kuma ya karanta wasullolin

i u o a ai au e

Ya gayyaci ɗalibbai su dauki shibtar a cikin kayyunansu.

# DARASI NA 7

1. **Tilawa bisa aikin baya**

Malami ya yi shibtar **e** da **ai** da **au**.

Ya gayyaci ɗalibbai a babban allo domin cin gyara

Bayan cin gyara malami ya karanta  kuma ya sa mafi yawan ɗalibbai su karanta.

2. **Aikin yau: karatu da rubutun baƙin l**

Malami ya gwada ɗalibbai hoto, ya tambaye su mi suka gani?
Ya ci gaba da tambayoyi har ya kai ga jumlar da za a aiki da ita.

## Mambobi sun lamunta da dokoki

Malami ya rubuta kalmar a babban allo.

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta:

lamunta

Ya sabko fadar dake ƙumshe da baƙin da za a aiki da shi.

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

la

l

Ya rubuta baƙin da babban rubutu

Ya gyyaci ɗalibbai su je babban allo su rubutu baƙin

l l l

Malami ya duba ya ci gyara bisa babban allo

l l l

Ya haɗa baƙin da wasulloli

Bayan ya haɗa su, sai ya karanta kuma ya sa a karanta faɗoɗin

| | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|
| li | lo | la | lu | le | lai | lau |

Ya sa ɗalibbai su rubuta waɗansu daga cikin faɗaoɗin bisa ƙananan allunan su

Kuma a ci gyara bisa babban allo.

li lau le lo

- A nemo sunayen da suka ƙaumshi sabon baƙin tare da yin la'akari da baƙaƙen da aka gani da kuma mahawarorin da aka yi.

allo - aula - alu - lalo - lailai

- Kowane ɗalibi ya rubuta sunan da ya samo a babban allo
- Ɗalibbai su karanta sunayen, da suka rubuta a babban allo
- Malami ya nuna ma ɗalibbai ire – iren rubutun baƙin l : ℓ : L
- Malami ya rubuta aikin da ɗalibbai za su dauka a cikin kayyunanasu.

| | | |
|---|---|---|
| l | l | l |

| | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|
| li | lu | lo | la | lai | lau | le |

| | |
|---|---|
| allo | aulo |

- Malami ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta
- Ya gayyaci ɗalibbai su ɗauki rubutun a cikin kayyunansu
- A ƙarshe ya gewaya domin cin gyara.

# DARASI NA 8

1. **Tilawa bisa aikin baya**

Malami ya yi shibtar baƙin **l** da faɗoɗin da suka ƙumshim baƙin

li   lo   la   lu   lai   lau

Ya gayyaci ɗalibbai a babban allo domin cin gyara.

Bayan cin gyara malami ya karanta kuma ya sa mafi yawan ɗalibbai su karanta.

2. **Aikin yau : Karatu da rubutun** t

Malami ya maimaita tambayoyi da ya wa ɗalibai lokacin hiddo jumilar baya don a samo kalmar da za a aiki da ita.

Kungiya ta yi tanadin arziki.

Malami ya rubuta kalmar a babban allo.

Ya karanta ya sa ɗalibbai su karanta :

tanadi

Ya sabko baƙin ƙarƙashen fadar.

Ya karanta ya sa ɗalibbai su karanta.

ta
t

Ya rubuta baƙin da babban rubutu.

Ya gayyaci ɗalibbai su je babban allo su rubuta baƙin

t   t   t

Malami ya duba ya ci gyara bisa babban allo ya haɗa baƙin da wasulloli.
Bayan ya haɗa su, sai ya karanta kuma ya sa a karanta faɗoɗin

ti   to   ta   tu   te   tai   tau

Ya sa ɗalibbai su rubuta waɗansu daga cikin faɗoɗin bisa ƙananan allunansu.

Kuma a ci gyara bisa babban allo.

ti to ta tu te tai tau

Ɗalibbai su nemo sunayen da suka ƙumshi sabon baƙi

talata tautau tuta tata tulu

- Kowane ɗalibi ya rubuta sunan da ya samo a babban allo
- Ɗalibbai su karanta sunayen, da suka rubuta a babban allo
- Malami ya nuna ma ɗalibbai ire - iren rubutun baƙin † : t : T : *t*
- Malami ya rubuta aikin da ɗalibbai za su dauka a cikin kayyunanasu.

t t t

ti tu to ta tai tau te

talata tulu

- malami ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta
- ya gayyaci ɗalibbai su ɗauki rubutun a cikin kayyunansu
- a ƙarshe ya gewaya domin cin gyara.

# DARASI NA 9

1. **Tilawa bisa aikin baya**

Malami ya yi shibtar baƙin **t** da faɗoɗin da suka ƙumshim baƙin

ti to ta tu tai tau

tautau tata

Ya gayyaci ɗalibbai a babban allo domin cin gyara.

Bayan cin gyara malami ya karanta kuma ya sa mafi yawan ɗalibbai su karanta.

2. **Aikin yau : Karatu da rubutun C**

Malami ya maimaita tambayoyi da ya wa ɗalibai lokacin hiddo kalmar baya don a samo kalmar da za a aiki da ita.

Adamu na cika takarda

Tahanyar hoto a hiddo kalmar da za a aiki da ita.

Malami ya rubuta sunan a babban allo.

Ya karanta ya sa ɗalibbai su karanta :

cika

Ya sabko fadar da ke kumshe da baƙinda za a aiki da shi .

Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

ci

Ya sabko wasalin ƙarƙashin fadar

Ya karanta, ya sa ɗalibbai su karanta

ci

c

Ya rubuta baƙin da babban rubutu.

Ya gayyaci ɗalibbai su je babban allo su rubuta baƙin

c c c

Malami ya duba ya ci gyara bisa babban allo ya haɗa baƙin da wasulloli.

Bayan ya haɗa su, sai ya karanta kuma ya sa a karanta faɗoɗin

ci co ca cu ce cai cau

Ya sa ɗalibbai su rubuta waɗansu daga cikin faɗoɗin bisa ƙananan allunansu.

Kuma a ci gyara bisa babban allo.

ci ca co

Ɗalibbai su nemo sunayen da suka ƙumshi sabon baƙi

cadi cuta ceto ci

- Kowane ɗalibi ya rubuta sunan da ya samo a babban allo
- Ɗalibbai su karanta sunayen, da suka rubuta a babban allo
- Malami ya nuna ma ɗalibbai ire - iren rubutun baƙin c : c : C:
- Malami ya rubuta aikin da ɗalibbai za su dauka a cikin kayyunanasu.

c c c

ci cu co ca

cuta ci

- malami ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta
- ya gayyaci ɗalibbai su ɗauki rubutun a cikin kayyunansu
- a ƙarshe ya gewaya domin cin gyara.

# DARASI NA 10

1. Tilawa bisa mahawara da aka yi

2. Aikin yau: karatu da rubutun : d

Malami ya gwada ma ɗalibbai hoto, ya tambaye su : mi su ka gani? kuma mi suka gane?

Ya ci gaba da tambayoyi har ya kai ga wannan amsa.

ya dace  a yi dokoki

Ta hanyar hoto a hiddo jumlar da za a aiki da ita.
Malami ya rubuta sunan a babban allo.
Ya karanta  kuma  ya sa ɗalibbai su karanta :

dace

Ya sabko fadar da ke kumshe da baƙinda  da za a aiki da shi .
Ya karanta  kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

da
d

Ya rubuta baƙin da babban rubutu.
Ya gayyaci ɗalibbai su je babban allo su rubuta baƙin

d d d

Malami ya duba ya ci gyara bisa babban allo ya haɗa baƙin da wasulloli.
Bayan ya haɗa su, sai ya karanta, kuma ya sa a karanta faɗoɗin

di do da du de dai dau

ya sa ɗalibbai su rubuta waɗansu daga cikin faɗoɗin bisa ƙananan allunansu.

Kuma a ci gyara bisa babban allo.

da du di dau

Ɗalibbai su nemo sunayen da suka ƙumshi sabon baƙi

**cida lada dodo dala dauda dila**

- Kowane ɗalibi ya rubuta sunan da ya samo a babban allo
- Ɗalibbai su karanta sunayen, da suka rubuta a babban allo
- Malami ya nuna ma ɗalibbai ire - iren rubutun baƙin d : d : D :
- Malami ya rubuta aikin da ɗalibbai za su dauka a cikin kayyunanasu.

| | | | |
|---|---|---|---|
| d | d | d | |
| di | da | du | dau |
| adadi | dace | | |

- Malami ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta,
- Ya gayyaci ɗalibbai su ɗauki rubutun a cikin kayyunansu,
- A ƙarshe ya gewaya domin cin gyara.

# <u>DARASI NA 11.</u>

1. **Tilawa bisa aikin baya**

Malami ya yi shibtar baƙin d da faɗoɗin da suka ƙumshi baƙin

di du da dai

cida dubu ladi

Ya gayyaci ɗalibbai a babban allo domin cin gyara.

Bayan cin gyara malami ya karanta kuma ya sa mafi yawan ɗalibbai su karanta.

2. **Aikin yau: karatu da rubutun : j**

Malami ya maimaita tambayoyi da ya wa ɗalibai lokacin hiddo jumlar baya don a samo sunan da za a aiki da shi.

## Malamin gona na jawabi kan tattalin baraji

jawabi

Malami ya gwada ma ɗalibbai hoto ya tambaye su : mi suke gani?
Kuma mi suka gane? Dan a samo wannan amsa.
Malami ya rubuta sunan a babban allo.
Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta :

jawabi

Ya sabko fadar da ke kumshe da baƙinda da za a aiki da shi .
Ya karanta ya sa ɗalibbai su karanta.

ja
j

Ya sabko wasali ƙarƙashin fadar.
Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta.

ja
j

Ya rubuta baƙin da babban rubutu.
Ya gayyaci ɗalibbai su je babban allo su rubuta baƙin

j j j

Malami ya duba ya ci gyara bisa babban allo ya haɗa baƙin da wasulloli. Bayan ya haɗa su, sai ya karanta, kuma ya sa ɗalibbai su karanta faɗoɗin

ji jo ja ju je jai jau

Ya sa ɗalibbai su rubuta waɗansu daga cikin faɗoɗin bisa ƙananan allunansu.

Kuma a ci gyara bisa babban allo.

ji jau jo ju

Ɗalibbai su nemo sunayen da suka ƙumshi sabon baƙin

jadi jiji

- Kowane ɗalibi ya rubuta sunan da ya samo a babban allo
- Ɗalibbai su karanta sunayen, da suka rubuta a babban allo
- Malami ya nuna ma ɗalibbai ire - iren rubutun baƙin j : j : J : *j*
- Malami ya rubuta aikin da ɗalibbai za su dauka a cikin kayyunanasu.

j j j

daji kauje

Dije ta je jeji

- malami ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta
- ya gayyaci ɗalibbai su ɗauki rubutun a cikin kayyunansu
- a ƙarshe ya gewaya domin cin gyara.

## DARASI NA 12

1. **Tilawa bisa aikin baya**

Malami ya yi shibtar baƙin j da faɗoɗin da suka ƙumshi baƙin

ji jo ja ju je jau

Ya gayyaci ɗalibbai a babban allo domin cin gyara.

Bayan cin gyara malami ya karanta kuma ya sa mafi yawan ɗalibbai su karanta.

2. **Aikin yau: karatu da rubutun : ɗ**

Malami ya maimaita tambayoyi da ya wa ɗalibbai lokacin hiddo jumlar baya don a samo sunan da za a aiki da shi.

### Shugaba ya ɗauko kayan ƙungiya

ɗauko

Malami ya gwada ma ɗalibbai hoto ya tambaye su : mi suke gani?
Kuma mi suka gane? Dan a samo wannan amsa.
Malami ya rubuta sunan a babban allo.
Ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta :

ɗauko

Ya sabko fadar da ke kumshe da baƙinda da za a aiki da shi .
Ya karanta ya sa ɗalibbai su karanta.

Bayan ya haɗa su sai ya karanta kuma ya sa ɗalibbai su karanta. Ɗalibbai su nemo sunayen da suka ƙumshi sabon baƙin tare da yin la'akari da baƙaƙen da ake gani.

fyace fyaɗe fyacewa

Kowane ɗalibi ya rubutan sunan da ya samo a babban allo. Ɗalibbai su karanta sunaye, kalmomi da suka rubuta bisa babban allo. Malami ya rubuta aikin da ɗalibbai za su ɗauka cikin kayyunansu.

fy fy fy

fyace fyaɗe fyacewa

Tamingo tana kyaɗar shinkafa

- Malami ya karanta ya sa ɗalibbai su karanta
- Ya gayayci su su ɗauki rubutun cikin kayyunansu
- Malami ya gewaya domin cin gyara.

# DARASI NA 41.

**Babbar tilawa**

- Malami ya ma ɗalibbai shibtar duk aikin da suka yi baya.
- A ci gyara a babban allo.
- Malami ya rubuta shibtar a tsabtace bisa babban allo.

Gwa gwa gwai

Kwi kwa kwai

ƙwi ƙwa ƙwai

tsi tsa tso tse tsu tsai tsau

fya

gwami ƙwayoyi tsari fyaɗe tsutsotsi

- Malami ya gayyaci waɗansu ɗalibbai su karanta, shi kuma ya karanta.
- Malami da ɗalibbai sun karanta matannan da ke cikin littafinsu.
- Malami ya yi la'karida duk aikin da suka yi baya domin tahiyar da tilawar ta ƙarshen aikin.

# LISSAHI

## <u>LITTAHIN MALAMI</u>

## TSARIN DARUSSAN LISSAHI

| Lambar darasi | Sunan darasi |
|---|---|
| Darasi na 1 | Koyon riƙon alkalami |
| Darasi na 2 | Koyon riƙon alkalami |
| Darasi na 3 | Karatu da rubutun lambobi da 1 zuwa 3 |
| Darasi na 4 | Karatu da rubutun lambobi da 4 zuwa 6 |
| Darasi na 5 | Karatu da rubutun lambobi da 7 zuwa 9 |
| Darasi na 6 | Tilawa |
| Darasi na 7 | ƙari marar ajiya na lambobi 1 zuwa 9 |
| Darasi na 8 | Ragi marar ajiya na lambobi 1 zuwa 9 |
| Darasi na 9 | Karatu da rubutun gomomi daga (10 – 90) |
| Darasi na 10 | Karatu da rubutun gomomi daga (11 – 99) |
| Darasi na 11 | Karatu da rubutun gomomi daga (100 – 900) |
| Darasi na 12 | Karatu da rubutun gomomi daga (101 – 999) |
| Darasi na 13 | Tilawa |
| Darasi na 14 | ƙari marar ajiya |
| Darasi na 15 | Ragi marar ajiya |
| Darasi na 16 | Karatu da rubutun dubbai (1000 – 9000) |
| Darasi na 17 | Karatu da rubutun lambobi daga (1001 – 9999) |
| Darasi na 18 | Karatu da rubutun gomomi dubbai (10.000 – 90.000) |
| Darasi na 19 | Karatu da rubutun lambobi (10.001 – 99.999) |
| Darasi na 20 | Tilawa |
| Darasi na 21 | ƙari mai ajiya |
| Darasi na 22 | Ragi mai ajiya |
| Darasi na 23 | Awon nauyi |
| Darasi na 24 | Awon tsawo |
| Darasi na 25 | Karatu da rubutun ɗaruruwan dubbai 100.000 – 900.000 |
| Darasi na 26 | Karatu da rubutun lambobi 100.001 – 999.999 |
| Darasi na 27 | Tilawa |
| Darasi na 28 | riɓi marar ajiya na lambobi 1 zuwa 9 |
| Darasi na 29 | Hayoyin koyon riɓi daga 0 zuwa 9 |
| Darasi na 30 | riɓi mai ajiya na lambobi 2 sama 1ƙasa |
| Darasi na 31 | riɓi mai ajiya na lambobi 2 sama 1ƙasa |
| Darasi na 32 | riɓi mai ajiya na lambobi 3 sama 1ƙasa |
| Darasi na 33 | Tilawa |
| Darasi na 34 | riɓi mai ajiya na lambobi 3 ko 4 sama 2ƙasa |
| Darasi na 35 | Karatu da rubutun miliyan |
| Darasi na 36 | Aiki bisa miliyan |
| Darasi na 37 | Rabawa marar ajiya na lambobi 1 zuwa 9 |
| Darasi na 38 | Rabawa marar ajiya mai lamba 2 ga wanda akka raba, 1 ga marabi |
| Darasi na 39 | Rabawa mai ajiya mai lamba 2 ga wanda akka raba, 2 ga marabi |
| Darasi na 40 | Rabawa mai ajiya mai lamba 3 ga wanda akka raba, 2 ga marabi |
| Darasi na 41 | Babbar tilawa |

Ja-goran tahiyar da darasin lissahi

| Ayukka da gurinsu | Ayukkan malami | Ayukkan ɗalibbai |
|---|---|---|
| I. tilawa | -Malami ya gewaya ya duba aikin da ya ba ɗalibbai su yi a gida<br>-Ya gayyace su su sa cin gyaran aikin a babban allo<br>-Ya gayyaci waɗanda ba su gama ba, su ɗauki gyararren aikin. | Su bada kayyuna su gwada ma malami<br><br>-Su ɗauka bayan cin gyara |
| II. Sabon aiki<br>1. Gabatarwa<br><br>2. Bayyanawa<br><br>Auni | Malami ya bada misalin baka don gabatar da aikinshi<br>-Malami ya gayyaci ɗalibbanshi su huddo gurin aikin<br>-Ya tabbatar da gurin aikin<br>-Malami ya tambayi ɗalibin da zai iya tahiya wajen babban allo ya buga lissahi<br>-Malami ya yi cin gyaran aikin ɗalibi<br>-In karatu da rubutun lambobi ne malami ya nuna dalla-dalla yadda ake rubuta lambobin.<br>-In buga lissahi ne, ya fara nuna masu lambar, sannan yadda ake buga lissahin dalla-dalla<br><br>Malami ya sa su aiki 2 zuwa 3 su yi a babban allo | -ɗalibbai su saurara<br><br>- su bada gurin<br><br>-Su saurare shi<br>-In an samu ya zo ya buga<br><br>-Su duba da kyau<br>-Su saurara, su duba<br><br>-Su saurara, su duba<br><br>-ɗalibbai su je da guda-guda su yi aikin a babban allo<br><br>-Su zo su ci-gyara |
| Larwai | -Malami ya sa a ci-gyaran aikin a babban allo<br>-Ya ba su aiki su yi bisa alluna<br>-Malami ya gewaya ya duba, don<br>-ya taimaki waɗanda ba su gane ba<br><br>-Malami ya ba su aikin yi bisa kayyuna ya gewaya ya duba<br><br>-Ya sa ci-gyara a babban allo.<br>-Ya gayyaci ɗaliban da ba su gama ba su ɗauki gyararren aikin cikin kayyuna, ya duba<br>-In aikin bisa karatu da rubutun lambobi ne, ya gayyace su, su ɗauki lambobi cikin kayyunansu.<br>-Ya ba su aikin yi a gida (aikin da ke cikin littahin ɗalibbai) | -Su aikata<br><br>-Su nuna allunansu<br><br>-Su ɗauka<br><br>-Su bada amsa<br>-Su ɗauki bayan cin gyara<br><br>Su ɗauki<br><br>Su ɗauki |

# DARASI NA 1

Koyon riƙon alkalami

Guri : ɗalibbai su ƙware ga iya riƙon alkalami da yin amfani da shi

.

l

/

C

N

O

DARASI NA 2

Sabon aiki :

Ci-gaba da koyon riƙon alkalami

Guri : ɗalibbai su ƙware ga iya riƙon alkalami da yin amfani da shi.

.

/

n

*s*

# DARASI NA 2

Koyon karatu da rubutun lambobi da 1 zuwa 3

1) Tilawa: A ɗan taɓa aiki bisa koyon riƙon alkalami.

2) Sabon aiki:

Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun lambar 1 da 2 da 3

- Malami ya bada misali kamar haka: kai nawa ke ga mutun?
- Dalibbai su bada amsa (kai 1)
- Ya shaida masu da lambar 1 za su koyon karantawa da rubutawa
- Ya zo ya rubuta a cin gyara
- Ya nuna masu dalla-dalla yadda ake rubuta lambar.

1 1 1

- Ya gayyaci ɗalibi 2 zuwa 3 su zo su koyi rubutun lambar a babban allo
- Ya ci-gyara
- Ya sa ɗalibban su koyi rubutun lambar a ƙananan alluna.
- Ya gewaya ya duba don taimakon waɗanda ba su gane ba
- Malami ya bi waɗannan hanyoyin don koyar da lambar 2 da 3. A ƙarshe ya gayyace su, su ɗauki rubutun lambobin cikin kayyuna karmar haka

1 1 1

2 2 2

3 3 3

# DARASI NA 3

Koyon karatu da rubutun lambobi daga 4 zuwa 6.

1.Tilawa: malami ya gewaya ya dubi aikin da ya ba su su yi a gida
Ya gayyace su, su ci-gyaran aikin a babban allo
Ya gayyaci ɗalibbai su ɗauka bayan cin gyara.

2. Sabon aiki

Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun lambar 4 da 5 da 6 :

- Malami ya bada misali kamar haka: doki ƙafa nawa gare shi?
- Dalibbai su bada amsa (ƙafa 4)
- Ya shaida masu da lambar 4 za su yi koyon karantawa da rubutawa
- Ya zo ya rubuta a ci gyara
- Ya nuna masu dalla-dalla yadda ake rubuta lambar.

4 4 4

- Ya gayyaci ɗalibi 2 zuwa 3 su zo su koyi rubutun lambar a babban allo
- Ya ci-gyara
- Ya gayyaci ɗalibban su koyi rubutun lambar a ƙananan alluna.
- Ya gewaya ya duba don taimako waɗanda ba su gane ba
- Malami ya bi waɗannan hanyoyin don koyar da lambar 5 da 6. A ƙarshe ya gayyace su, su ɗauki rubutun lambobin cikin kayyuna karmar haka

4 4 4

5 5 5

6 6 6

# DARASI NA 4

Koyon karatu da rubun lambobi daga 7 zuwa 9.

1.Tilawa: malami ya bi hanyoyi da aka nuna mashi don shirya tilawa.

2. Sabon aiki

Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun lambar 7 da 8 da 9 :

- Malami ya bada misali kamar haka: cikin sati kwana nawa ne?
- Dalibbai su bada amsa (kwana 7)
- Ya shaida masu da lambar 7 za su yi koyon karantawa da rubutawa
- Ya zo ya rubuta a cin gyara
- Ya nuna masu dalla-dalla yadda ake rubuta lambar.

7 7 7

- Ya gayyaci ɗalibi 2 zuwa 3 su zo su koyi rubutun lambar a babban allo
- Ya ci-gyara
- Ya sa ɗalibban su koyi rubutun lambar a ƙananan alluna.
- Ya gewaya ya duba don taimako waɗanda ba su gane ba
- Malami ya bi waɗannan hanyoyin don koyar da lambar 8 da 9. A ƙarshe ya gayyace su, su ɗauki rubutun lambobin cikin kayyuna karmar haka

7 7 7

8 8 8

9 9 9

# DARASI NA 5

1. Tilawa

Guri:ɗalibbai su ƙarfafa iliminsu cikin darussan nan 5 da suka koya (bisa karatu da rubutun lambobi daga 1 zuwa 9).

Tahiyar da aiki:
-Malami ya yi masu shibtar lambobi bisa ƙananan alluna :

2 . 4 5 . 7

-Ya gewaya ya duba, ana yi ana cin-gyara a babban allo
-Ya yi masu wata shibta cikin kayyuna:

1 - 3 - 8 -

-Ya gewaya ya duba ya ci-gyara a babban allo
-Waɗanda ba su gano ba su ɗauki gyararren aikin cikin kayyuna.

# DARASI NA 6 :

Ƙari marar ajiya daga 1 zuwa 9

1. Tilawa : Malami ya yi ma ɗalibbai shibtar lambobi daga 1 zuwa 9(bisa ƙananan alluna).
    - Ana yi ana cin-gyara
    - A yi karatun lambobi

2. Sabon aiki:

Guri; ɗalibbai su iya buga lissahin ƙari marar ajiya da lambobi daga 1 zuwa 9.

Yadda za a tahiyar da aiki :

-Malami ya bada misali da ya dace don hiddo gurin aiki
-Malam Sule ya sayi dashe 3, daga baya ya ƙaro 5, nawa kenan?
-Dalibbai su bada amsa 8
-Malami ya tambaye su yadda suka samo 8
-Ya faɗa masu gurin darasi : ƙari marar ajiya
-Ya tambaye su wanda ya iya aza lissahi, ya zo a babban allo ya yi, a ci gyara.
-Malami ya nuna masu alamar ƙari
Ya nuna masu yadda ake aza lissahi, da inda ake rubuta alamar ƙari, wurin sandar tsaida lissahi, da inda ake sa jimillar.

Misali

$$\begin{array}{r} 5 \\ +\ 3 \\ \hline 8 \end{array}$$

-Ya bada ajin lissahi 2 ko 3 a babban allo, ɗalibbai su zo su yi da guda-guda ; a ci-gyara

$$\begin{array}{r} 4 \\ +\ 1 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 3 \\ +\ 3 \\ \hline \end{array}$$

Ya ba su aiki su yi bisa ƙananan alluna

$$\begin{array}{r} 2 \\ +\ 6 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 4 \\ +\ 5 \\ \hline \end{array}$$

- Ya gewaya ya duba
- A ci-gyara a babban allo
- Ya ba su aiki su yi cikin kayyuna

$$\begin{array}{r} 2 \\ +\ 1 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 3 \\ +\ 4 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 5 \\ +\ 2 \\ \hline \end{array}$$

- Ya gewaya, ya duba, a ci-gyara a babban allo
- Ya ba su aikin yi a gida.

# DARASI NA 7

Ragi marar ajiya

1. Tilawa : Malami ya gewaya ya duba aikin da ɗalibbai suka yo a gida.
-A ci-gyaran aikin a babban allo
-Dalibban da ba su gamo ba su gyara cikin kayyuna.

2.Sabon aiki:

Guri; ɗalibbai su iya buga lissahin Ragi marar ajiya da lambobi daga 1 zuwa 9.

Yadda za a tahiyar da aiki :

-Malami ya bada misali da ya dace don hiddo gurin aiki
-Malam Sahabi ya sayo buhu 6 na hatsi, ya yi ƙyauta da 2, nawa suka yi mashi saura?
-Dalibbai su bada amsa 4
-Malami ya tambaye su yadda suka samo 4
-Ya faɗa masu gurin darasi : ragi marar ajiya
-Ya tambaye su wanda ya iya aza lissahi, ya zo a babban allo ya yi, a ci gyara.
-Malami ya nuna masu alamar ragi
Ya nuna masu yadda ake aza lissahi, da inda ake rubuta alamar ragi, wurin sandar tsaida lissahi, da inda ake sa saura.

Misali

$$\begin{array}{r} 6 \\ -\ 2 \\ \hline 4 \end{array}$$

-Ya bada ajin lissahi 2 ko 3 a babban allo, ɗalibbai su zo su yi da guda-guda ; a ci-gyara

$$\begin{array}{r} 4 \\ -\ 1 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 4 \\ -\ 2 \\ \hline \end{array}$$

Ya ba su aiki su yi bisa ƙananan alluna

$$\begin{array}{r} 3 \\ -\ 1 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 8 \\ -\ 3 \\ \hline \end{array}$$

- Ya gewaya ya duba
- A ci-gyara a babban allo
- Ya ba su aiki su yi cikin kayyuna

$$\begin{array}{r} 7 \\ -\ 5 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 8 \\ -\ 4 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 6 \\ -\ 2 \\ \hline \end{array}$$

- Ya gewaya, ya duba, a ci-gyara a babban allo
- Ya ba su aikin yi a gida

# DARASI NA 8

Karatu da rubutun gomomi

2. Tilawa : Malami ya gewaya ya duba aikin da ɗalibbai suka yo a gida.
-A ci-gyaran aikin a babban allo
-Dalibban da ba su gamo ba su gyara cikin kayyuna.

2.Sabon aiki:

Guri; ɗalibbai su iya karatu da rubutun gomomi.

Yadda za a tahiyar da aiki
-Malami ya bada misali da ya dace don hiddo gurin aiki
-wutar daji ta ƙone dame 7 gonar sani da wasu 3 na maƙwabcinshi, dame nawa suka ƙone?
-Dalibbai su bada amsa 10
-Malami ya tambaya su yadda suka samo 10
-Ya fada masu gurin darasi : koyon karatu da rubutun gomomi
-Ya tambaye su wanda ya iya rubuta lambar 10 a babban allo, a ci gyara.
-Malami ya rubuta da kyau ƙauyen babban allo, ya karanta ya sa su karanta
Ya nuna masu dalla-dalla yadda ake rubuta lambar .

| Gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|
| 1 | 0 |

-Ya ba su bayyanin lambar banza (0) da ake kira sifili (tana zaman ɗiyan lissahi, 1 na zaman gomomi.
Ya gayyaci 2 ko 3 a babban allo, ɗalibbai su zo su koyi rubuta lambar a babban allo da guda-guda. Ana yi ana cin-gyara.
Ya sa su rubuta bisa ƙananan alluna
Ya gewaya ya duba don taimakon waɗanda ba su gane ba
Ya bi waɗannan hanyoyin don koyar da sauran lambobi (20 30 40 50 60 70 80 90)

| G | ɗl |
|---|---|
| 1<br>2<br>3 | 0<br>0<br>0 |

- A ƙarshe ya sa su rubuta lambobin cikin kayyuna
- Ya gewaya ya na dubawa.

10 10 10 10

20 30 40 50 60 70 80 90

# DARASI NA 9

Karatu da rubutun lambobi daga 11 zuwa 99

3. Tilawa : Malami ya yi ma ɗalibbai shibtar lambobi daga 10 zuwa 90
-A ci-gyaran aikin a babban allo

2.Sabon aiki:

Guri; ɗalibbai su iya karatu da rubutun lambobi daga 11 zuwa 99.

Yadda za a tahiyar da aiki
-Malami ya bada misali da ya dace don hiddo gurin aiki
-wutar daji ta ƙone dame 6 gonar sani da wasu 5 na maƙwabcinshi, dame nawa suka ƙone?
-Dalibbai su bada amsa 11
-Ya faɗa masu gurin darasi : koyon karatu da rubutun lambobi daga 11 zuwa 99
Ya nuna masu dalla-dalla yadda ake rubuta lambar .

Ya gayyaci 2 ko 3 a babban allo, ɗalibbai su zo su koyi rubuta lambar a babban allo da guda-guda. Ana yi ana cin-gyara.

| G | ɗl |
|---|---|
| 1<br>2 | 1<br>5 |

- Malami ya bi hanyoyin da ya saba don koyar da sauran lambobi
- Ya shirya masu lambobi da za su ɗauka cikin kayyuna.

11 25 38 54

63 69 76 85 89

96 98 99

# DARASI NA 10

Karatu da rubutun ɗaruruwa da 100 zuwa 900

4. Tilawa : Malami ya yi ma ɗalibbai shibtar lambobi daga 11 zuwa 99
-A ci-gyaran aikin a babban allo

2.Sabon aiki:
Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun daruruwa daga 100 zuwa 900.
Yadda za a tahiyar da aiki
-Malami ya bada misali da ya dace don hiddo gurin aiki
-Misali sani ya hiddo kan dawa 65 kuma ya karo wasu 35 , kan dawa nawa suka zama?
-Dalibbai su bada amsa 100
-Ya faɗa masu gurin darasi : koyon karatu da rubutun daruruwa daga 100 zuwa 900
Bayan haka ya gayyaci wani ɗalibi ya zo ya buga lissahi a babban allo

$$\begin{array}{r} 65 \\ +\ 35 \\ \hline \end{array}$$

Ya tambayi ɗalibbai lamba nawa jimillar ta ƙumsa?
Ya jawo hankalinsu kan gidajen da suke cikin gidan ɗiyan lissahi a dama

Gomomi (a tsaka)
ɗaruruwa ( a hagun)

| ɗaruruwa | Gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|---|
| 1 | 0 | 0 |

Sai kuma malami ya ce masu: wannan lambar ɗari (100 kenan)
-Malami ya gayyaci wasu ɗalibbai su zo su rubuta 100 a babban allo, sa'annan kowa ya rubuta bisa allonshi. Ya gewaya layi-layi don ya taimaki waɗanda suka gaza.
Bayan haka ya rubuta masu lamba 200 cikin wani sashen a babban allo, kuma ya gayyaci wani ya rubuta ta cikin gidajen ɗiyan lissahi

| ɗaruruwa | Gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|---|
| 1 | 0 | 0 |
| 2 | 0 | 0 |

Matakan da ya bi wajen rubutun 100, 200, da 300 su zai bi har ya kai 900, (400, 500, 600, 700, 800, 900)
A kowace lamba, ya gayyace su, su rubuta a allunansu
A ƙarshe ya sa a rubuta lambobi duka cikin kayyunansu.

# DARASI NA 11

Karatu da rubutun lambobi da 101 zuwa 999

5. Tilawa : Malami ya yi ma ɗalibbai shibtar daruruwa cikin gidajensu.
(100, 300, 700, 900)

2.Sabon aiki:
Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun lambobi daga 101 zuwa 999.
-Malami ya gayyaci wani ɗalibi don ya rubuta mashi 100 a babban allo kuma ya samu wani ya rubuta 101.bayan haka sai ya sa shi ya rubuta wannan lambar cikin gidajen lambobi kamar haka:

| ɗaruruwa | Gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|---|
| 1 | 0 | 0 |
| 1 | 0 | 1 |
| 2 | 0 | 0 |

Kuma ya sa su rubuta 101 bisa allunansu. Malami ya bi wannan mataki har ya kai 999.
Malami ya gayyaci ɗalibbai su rubuta lambobi da za ya ba su, domin su tsara su cikin gidaje dan ya tabbatar da sun gane.

Misali : 237, 497, 889, 662, 999.

# DARASI NA 12

2. Tilawar sati

Guri:ɗalibbai su ƙarfafa iliminsu bisa rubutun lambobi, gomomi da ɗaruruwa da ƙari da ragi marar ajiya.

Tahiyar da aiki :

-Malami ya shirya gidajen lambobi (dl, gomomi, da ɗaruruwa). ɗalibbai su cika gidajen, ana yi ana cin gyara

| ɗaruruwa | gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|---|
| <br>3<br>5 | 1<br>0<br>2 | 0<br>1<br>4 |

-Ya yi masu shibtar wasu lambobi a ƙananan alluna ana yi, ana cin gyara

26 - 37 - 508 - 483 872 -

-Ya maimaita masu yadda ake ƙari da ragi marar ajiya ( da misalai)
-A ba su aikin yi a babban allo da a ƙananan alluna ana yi, ana cin-gyara.

$$\begin{array}{r} 4 \\ +\ 4 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 7 \\ +\ 1 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 8 \\ -\ 5 \\ \hline \end{array}$$

# DARASI NA 13

ƙari marar ajiya

Tilawa bisa aikin baya

Sabon aiki

Guri: koyon buga lissahi ƙari marar ajiya

Malami ya bada misali lissahin ƙari marar ajiya a babban allo.

```
   721
+  264
-------
```

Ya sa wani ɗalibi ya buga mashi lissahin, in ya kasa, malami ya buga da kanshi.
Ya ɗora masu wani lissahin 2 ko 3.

```
   542        675        520
+  335     +  227     +  103
-------    -------    -------
```

Ya sake ba ɗalibbai wani aikin su yi bisa allunansu.

```
   434        612        785
+  254     +  387     +  214
-------    -------    -------
```

Ya tura ɗalibbai da guda-guda a babban allo su je su gyara aikin, waɗanda ba su gamo ba su gyara.
Ya diba
A ƙarshe ya ba su aikin yi a gida.

```
  123     456      800      765
+ 776   + 543    + 199    + 234
-----   -----    -----    -----
```

# DARASI NA 14

Ragi marar ajiya

Tilawa bisa aikin baya

Sabon aiki

Guri: koyon buga lissahi ragi marar ajiya

Malami ya bada misali lissahin ragi marar ajiya a babban allo.

```
   721
-  264
```

Ya sa wani ɗalibi ya buga mashi lissahin, in ya kasa, malami ya buga da kanshi.
Ya ɗora masu wani lissahin 2 ko 3.

```
   542       675       520
-  331    -  220    -  100
```

Ya sake ba ɗalibbai wani aikin su yi bisa allunansu.

```
   434       612       785
-  214    -  310    -  214
```

Ya tura ɗalibbai da guda-guda a babban allo su je su gyara aikin, waɗanda ba su gamo ba su gyara.
Ya diba
A ƙarshe ya ba su aikin yi a gida.

```
   123      456      800      765
-  111   -  343   -  700   -  234
```

# DARASI NA 15

Karatu da rubutun dubbai da 1000 zuwa 9000

1.Tilawa : Malami ya yi tilawar aikin baya.

2.Sabon aiki:

Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun dubbai.

Malami ya samu misali kamar haka:
Kantin maganin dabbobi na da allunan huji 999, shugaban kantin ya ƙara allura 1
Allura nawa gare su gaba ɗaya?

$$\begin{array}{r} 999 \\ +\quad 1 \\ \hline = 1000 \end{array}$$

Malami ya soma daga hannun dama ya ce :

9 an ƙara 1 shi ya yi 10. a rubuta ƙasan lissahi (0) a gidan ɗiyan lissahi, a kai gomar nan 1 a gidan gomomi ajiya.

Gomar nan da aka kai ajiya an ƙara da 9 ta gidan gomomi shi ya yi 10. a rubuta 0 a gidan gomomi a kai 1gomar nan a gidan ɗaruruwa.

A ƙarshe gomar nan da aka kai gidan ɗaruruwa ajiya ita za a haɗa da 9 ta gidan ɗadi shi ya yi 10. Mun san ba a iya rubuta lamba 2 gida guda, sai mu ƙara sabon gidan guda (wato na 4) mu sa 1 nan.

$$\begin{array}{r} 999 \\ +\quad 1 \\ \hline = 1000 \end{array}$$

Wannan jimillar ita ake ce ma dubu. Ya tambayi ɗalibai inda suka ga irin wannan lamba.

Su ce mashi jikka (tamma 1000)

Bayan haka malami ya rubuta lambar 2000 a ƙauyen babban allo, sa'annan ya sa wani ɗalibi ya rubuta ta cikin gidan lambobi kamar haka :

| Dubbai | ɗaruruwa | gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|---|---|
| 1 | 0 | 0 | 0 |
| 2 | 0 | 0 | 0 |

Matakan da ya bi a baya, su zai ya bi don ya koya karatu da rubutun 3000, 4000
5000, 6000, 7000, 9000.
Malami ya ba su aiki su yi bisa allunansu
A ƙarshe ya ba su aikin da za su yi a gida a cikin kayyunansu.

# DARASI NA 16

Karatu da rubutun dubbai da 1001 zuwa 9999

1.Tilawa : Malami ya yi tilawar aikin baya.

2.Sabon aiki:

Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun lambobi daga 1001 zuwa 9999.

Malami ya gayyaci wani ɗalibi don ya rubuta mashi 1000 a babban allo kuma ya samu wani ya rubuta 1001.bayan haka sai ya sa shi ya rubuta wannan lambar cikin gidajen lambobi kamar haka:

| Dubbai | ɗaruruwa | gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|---|---|
| 1 | 0 | 0 | 0 |
| 1 | 0 | 0 | 1 |

Matakan da ya bi a baya, su zai ya bi don ya koya karatu da rubutun 3345, 4050 5010, 6600, 7008, 9999.

Malami ya ba su aiki su yi bisa allunansu

A ƙarshe ya ba su aikin da za su yi a gida a cikin kayyunansu.

# DARASI NA 17

Karatu da rubutun gomomin dubbai da 10000 zuwa 90000

1.Tilawa : Malami ya yi tilawar aikin baya.

2.Sabon aiki:

Guri: ɗalibbai su iya karatu da rubutun lambobi daga 10000 zuwa 90000.

Malami ya bi matakan da ya bi a bayan, yako masu karatu da rubutun 10000 zuwa 90000

$$
\begin{array}{r} 9999 \\ +\quad 1 \\ \hline = 10000 \end{array}
$$

Na biyu, ya bi ta nan :

10.000
20.000
30.000
90.000

Sa’annan ya bada aiki kamar haka su ɗauki cikin kayyunansu

40.000, 50.000, 60.000, 70.000, 80.000

# DARASI NA 18

Karatu da rubutun gomomin dubbai da 10001 zuwa 99999

1.Tilawa : Malami ya masu shibtar lambobi kamar haka: 20000, 40000, 50000, 90000.

2.Sabon aiki:

Guri: karatu da rubutun lambobi daga 10.001 zuwa 99999.

Malami ya gayyaci wani ɗalibi don ya rubuta mashi 10000 a babban allo kuma ya sa wani ya rubuta 10.001.bayan haka sai ya sa shi ya rubuta wannan lambar cikin gidajen lambobi kamar haka

10.001
10.081
31.599

Malami ya bi wannan mataki har ya kai ga lambar 99.999
Malami ya ba su aikin yi a gida.

63.0007, 80.978, 11.111, 78.432.

# DARASI NA 19

1.Tilawa

Guri:ɗalibbai su ƙarfafa iliminsu bisa rubutun lambobi, dubbai, da gomomi dubbai da ƙari da ragi marar ajiya.

Tahiyar da aiki :

- Malami ya shirya gidajen lambobi (dubbai, da gomomi dubbai). ɗalibbai su cika gidajen, ana yi ana cin gyara

| Gomomi dubbai | dubbai | ɗaruruwa | gomomi | ɗiyan lissahi |
|---|---|---|---|---|
| 1<br>5 | 0<br>2 | 0<br>3 | 0<br>4 | 0<br>4 |

- Ya yi masu shibtar wasu lambobi a ƙananan allunansu ana yi, ana cin gyara

26345 - 78137 - 48397 89832 -

- Ya maimaita masu yadda ake ƙari da ragi marar ajiya ( da misalai)
- YA ba su aikin yi a babban allo da ƙananan alluna ana yi, ana cin-gyara.

Aikin yi a gida

```
  41.56 4        12.6547        56.758
+ 4 3.124      + 15.2232      - 35.358
```

# DARASI NA 20

Kari mai ajiya

Tilawa: Malami ya ma ɗalibbai shibtar lambobi

Misali : 10.003, 25.330, 42.000, 99893
Ana yi ana cin-gyara

Sabon aiki

Guri ; ɗalibbai su iya buga lissahi ƙari mai ajiya

Yadda za a tahiyar da aikin

Malami ya bada misalin don hiddo aiki

Misali : likitan dabbobi na garin Kwaɓo, ya yi ma bisa 45 magani na tsutsar ciki, daga baya sun je garin Gwanɓa sun yi ma bisa 37magani.
Bisa nawa suka yi ma magani ?

- ɗalibbai su bada amsa
- ya shaida masu da za su aiki bisa ƙari mai ajiya
- ya tambayi wanda zai iya, ya zo ya buga lissahi, malami ya ci gyara.
- ya nuna masu dalla-dalla yadda ake buga lissahi.

```
   45
 + 37
 ----
   82
```

Ya ba su aikin yi a babban allo (aiki 2 zuwa 3)

```
   25      43      36
 + 16    + 58    + 15
 ----    ----    ----
```

Ana yi ana cin-gyara
Ya ba su aiki su yi a ƙananan alluna

```
   49      57        69
 + 14    + 48      + 22
 ----    ----      ----
```

ya gewaya, ya duba, a ci gyara
ya ba su aiki su yi cikin kayyuna, ya gewaya ya duba a ci-gyara

Ya ba su aikin yi a gida.

```
   34      43      55
 + 66    + 97    + 22
 ----    ----    ----
```

# DARASI NA 21

Ragi mai ajiya

Tilawa: Malami ya gewaya ya duba aikin da ya bada a yi a gida

A ci-gyara a babban allo
ɗalibbai da ba su gamo ba su gyara cikin kayyuna

Sabon aiki

Guri ; ɗalibbai su iya buga lissahi ragi mai ajiya

Yadda za a tahiyar da aikin

Malami ya bada misalin don hiddo aiki

Misali : A cikin gidan saida magani daɓɓoɓi na garin Abalak a ƙwai magani kashe tsutsar ciki ƙwaya 86 an saida ƙwaya 49, nawa suka yi saura ?

- ɗalibbai su bada amsa
- ya shaida masu da za su aiki bisa ragi mai ajiya
- ya tambayi wanda zai iya, ya zo ya buga lissahi, malami ya ci gyara.
- ya nuna masu dalla-dalla yadda ake buga lissahi.

```
   45
 - 37
 ----
   08
```

Ya ba su aikin yi a babban allo (aiki 2 zuwa 3) ana yi ana cin gyara

```
   25      43      61
 - 16    - 38    - 34
 ----    ----    ----
```

Ya ba su aiki yi a ƙananan alluna ana yi ana cin-gyara

```
   41      57      61
 - 14    - 48    - 27
 ----    ----    ----
```

ya gewaya, ya duba, a ci gyara

ya ba su aiki su yi cikin kayyuna, ya gewaya ya duba a ci-gyara

Ya ba su aikin yi a gida.

# DARASI NA 22

Awon nauyi

1.Tilawa : Malami ya bi hanyoyin da ya saba don tahiyar da tilawa

2.Sabon aiki
-Malami ya yi ma ɗalibbai tambaya

Misali : Da mi ake awon nauyi
-ɗalibbai su bada amsa (kilo)
-Ya nuna masu yadda ake rubuta kilo (kg) ta hanyar taƙaicewa; kg
-ɗalibbai su koya bisa babban allo da ƙananan alluna ana yi ana cin-gyara
ya nuna masu yadda ake rubuta kiluluwa daban daban (2kg, 5kg, 3kg, 20kg) tare da mahimman misalai

Misali: kwalin sukari (1kg)
Buhun gishiri (25kg)
Buhun shinkafa (50kg)
Tiyar hatsi (2kg da rabi)
Malami ya yi bayyani bisa tan
Tan1 = 1000kg
3000kg = ….tan ?
ya ba su aikin yi a gida

# DARASI NA 23

Awon tsawo

1.Tilawa : Malami yamaimaita aikin baya.

2.Sabon aiki
-ɗalibbai su san hanyoyin ma'aunin tsawon.

Misali : Da mi maɗinki ke awon yadi?
-ɗalibbai su bada amsa (metir)
-Ya nuna masu yadda ake rubuta metir ta hanyar taƙaicewa; m
-ɗalibbai su koya bisa babban allo da ƙananan alluna
km 1 m?
1000m km?
Ya ba su bayyani bisa eka
Eka shi ne takin ƙato ɗari 100 bisa ɗari 100
Takin ƙato shi ne kimanin metir ɗaya
Ya ba su aikin yi a gida

# DARASI NA 24

Awon yawan kalanzir, ruwa da sauransu

1.Tilawa : bisa awon tsawo

2.Sabon aiki)
Guri: ɗalibbai su san hanyoyin ma'aunin mai da sauransu
Tahiyar da aiki

Malami ya yi masu tambaya kamar haka
Da mi ake awon mai ? ɗalibbai su bada amsa (litar)
-Ya shaida masu gurin aiki ya ba su bayyani bisa ma'auni tsawo
-ya tambayi in aƙwai wanda ya iya rabuta litar a taƙaice ($\ell$) ya ci gyara.
Ya ba su bayyani bisa litar
Malami ya bada bayyani bisa duk abinda ake iya aunawa da litar
Misali : kalanzir, ruwa isansi gazuwal man shanu
Ya nuna masu da cewa litar guda 100cl
Ya ba su aikin yi a babban allo da kuma ƙananan alluna
Garuwar kalanzir litar nawa ne? Litar 18 zuwa 20
Tano litar nawa ne ? litar 200
Banda litar akwai wa su abubuwan awo : dekalitar (dal) litar10
Ekttolitar (hl) litar 100 ko rabin tano
A bada aikin gida bisa waɗannan ma'auni.

Awon tsawo
Ya ba su bayyani bisa eka
Eka shi ne takin ƙato ɗari (100) bisa ɗari (100)
Takin ƙato shi ne kimanin metir ɗaya
Ya ba su aikin yi a gida

# DARASI NA 25

Karatu da rubutun lambobi daga 100.001 zuwa 999.999

**Tilawa**

Malami ya yi masu shibtar lambobi ko su ccika gidajen lambobi.

**Sabon aiki**

Guri: koyon karatu da rubutun lambobi 100.001 zuwa 999.999 :

- Malami ya bi hanyoyin da ya bi ya koyar da lambobi 100.001 zuwa 999.999

Misali: 100.001
235.762

- Malami ya ba su aiki bisa babban allo su yi a ci-gyara

Ya sake ba su aikin yi a gida. Kamar haka su sa cikin gidajen lambobi a cikin kayyunansu.

248.800, 100.101, 804.625, 958.562

# DARASI NA 26

## Sabon aikin

Guri : Malami ya maiamaita darussan sati da ya wuce
Inda ya ga ɗalibbai na da matsala zai bada ƙarfi, ya yi aiki da hanyoyin ja-goron tilawa.

## Tahiyar da aiki

Malami ya shirya gidajen lambobi (ɗaruruwan ɗubbai ƙari da ragi mai ajiya, awon nauyi da tsawo).

| ɗd | gd | d | ɗ | g | dl |
|---|---|---|---|---|---|
| 1<br>2 | 0<br>0 | 0<br>0 | 0<br>0 | 0<br>0 | 0<br>0 |

Ya ba su waɗansu lambobi don cika gidajen lambobi
Ya ba su aiki bisa ƙari da ragi mai ajiya

```
   63.214        43.765        73.215        98.645
+  25.896      + 46.478      - 62.037      - 87.596
```

kwalin sukari  kilo nawa ne ?
buhun shinkafa kilo nawa ne ?
tan guda kilo nawa ne?
km metir nawa ne?
Eka1 tsawon m nawa bisa nawa ne ?

# DARASI NA 27

Riɓi marar ajiya na lambobi daga 1 zuwa 9

2.Sabon aiki:

Guri; koyon riɓi marar ajiya da lambobi daga 1 zuwa 9.

Misali: Macce 3 sun kawo ma likitansu kowace, koshiya 2 ta garin kokon yara.
Koshiya nawa likitan ya samu ?

Ta hanyar ƙari, ga yanda zai yi :

- Maimakon a ce 222 gara a ce 2 an riɓinya ta so 3
- sai malami ya ce : 2 an riɓinya ta so 3, shi ya yi 6
- ya riƙa gwada abinda yake karantawa
- sandar tsaida lissahi, da inda ake sa saura.

Misali 2 + 2 + 2 =6

$$\begin{array}{r} 2 \\ \times\ 3 \\ \hline 6 \end{array}$$

-Ya aika ɗalibi 2 ko 3 su yi ajin waɗansu lissahinn riɓi a babban allo

misali :

$$\begin{array}{r} 4 \\ \times\ 1 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 4 \\ \times\ 2 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 3 \\ \times\ 3 \\ \hline \end{array}$$

Ya ba ɗalibbai aiki su yi cikin allunansu

$$\begin{array}{r} 3 \\ \times\ 2 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 4 \\ \times\ 0 \\ \hline \end{array} \qquad \begin{array}{r} 3 \\ \times\ 3 \\ \hline \end{array}$$

Ya gewaya layi- layi don ya ga waɗanda ba su gane ba
Ya tura ɗalibbai da dai-daya a babban allo su ci-gyara kuma su diba
Ya ba su aikin yi a gida a ƙarshe.

# DARASI NA 28

Hanyoyin koyon riɓi da 0 zuwa 9

Tilawa
Malami ya yi tilawar aikin baya

Sabon aiki
Guri: koyon hanyoyin riɓi.

| | | |
|---|---|---|
| 1 x 0 = 0 | 2 x 0 = 0 | 3 x 0 = 0 |
| 1 x 1 = 1 | 2 x 1 = 2 | 3 x 1 = 3 |
| 1 x 2 = 2 | 2 x 2 = 4 | 3 x 2 = 6 |
| 1 x 3 = 3 | 2 x 3 = 6 | 3 x 3 = 9 |
| 1 x 4 = 4 | 2 x 4 = 8 | 3 x 4 = 12 |
| 1 x 5 = 5 | 2 x 5 = 10 | 3 x 5 = 15 |
| 1 x 6 = 6 | 2 x 6 = 12 | 3 x 6 = 18 |
| 1 x 7 = 7 | 2 x 7 = 14 | 3 x 7 = 21 |
| 1 x 8 = 8 | 2 x 8 = 16 | 3 x 8 = 24 |
| 1 x 9 = 9 | 2 x 9 = 18 | 3 x 9 = 27 |
| 1 x 10=10 | 2 x 10=20 | 3 x 10=30 |

Malami ya sa ɗalibbai su ɗauki allon riɓi a cikin kayyunansu su je gida su karance shi a kai.

# DARASI NA 29

Riɓi marar ajiya mai lamba 2 sama 1 ƙasa

1.Tilawa malami ya yi ma ɗalibbai tamboyoyi bisa hanyoyi riɓi, su ba shi amsa bisa alluna. Ana yi ana cin gyara a babban allo.

2.Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su iya buga lissahin riɓi marar ajiya mai lamba 2 sama, 1 ƙasa.

Yadda malami zai tahiyar da aiki
Malami ya bada misali:

Malam Laminou ya yi kwana 3 yana kai taki gona cikin amalanke, kowace rana yana yin sau 13. sau nawa ya yi ?
ɗalibbai su bada amsa
malami ya gaya masu gurin aikinshi ; riɓi marar ajiya mai lamba 2 sama 1 ƙasa
ya tambayi ɗalibin da zai iya nuga lissahi a babban allo, ya zo ya buga malami ya ci-gyara. Ya nuna masu yadda ake buga lissahi dalla-dalla

Ya ba su aikin yi bisa babban allo

```
  13
X  3
----
```

```
  12          13
x  4        x  3
----        ----
```

ya ba su aikin yi bisa kayyunansu da alluna

```
  27          13          11
x  4        x  2        x  5
----        ----        ----
```

ya ba su aikin yi a gida

```
  24          31          50
x  2        x  3        x  1
----        ----        ----
```

# DARASI NA 30

Riɓi mai ajiya mai lamba 2 sama 1 ƙasa

Tilawa malami ya gewaya ya duba aikin da ya ba ɗalibbai an yi a gida.

Ana yi ana cin gyara a babban allo
ɗalibbai da ba su gamo ba su gyara cikin kayyuna.

Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su iya buga lissahin riɓi mai ajiya mai lamba 2 sama, 1 ƙasa.

Yadda malami zai tahiyar da aiki
Malami ya bada misali: don hiddo gurin aiki

Misali : mutun 15 sun kwaso don haɗawa a yi takin tsime, kowanensu ya yi mayawa 3. mayawa nawa suka yi su duka ?
ɗalibbai su bada amsa
malami ya gaya masu gurin aikinshi ; riɓi mai ajiya mai lamba 2 sama 1 ƙasa
ya tambayi ɗalibin da zai iya buga lissahi a babban allo, ya zo ya buga malami ya ci-gyara.
Ya nuna masu yadda ake buga lissahi dalla-dalla.

```
  15
x  3
----
  45
```

Ya ba su aikin yi bisa babban allo (ɗalibi 2 zuwa 3) su zo su buga ana yi, ana cin gyara.

```
  16        14        13
x  7      x  4      x  5
----      ----      ----
```

ya ba su aikin yi bisa ƙananan alluna. Ya gewaya ya duba a ci gyara.

```
  44        15        45
x  6      x  9      x  5
----      ----      ----
```

ya ba su aikin yi cikin kayyuna, ya gewaya ya duba a ci gyara a babban allo.

```
  38        56        83
x  2      x  4      x  5
----      ----      ----
```

ya ba da aikin da ɗalibbai za su yi a gida

## DARASI NA 31

Tilawa :

Guri : ɗalibbai su ƙara ƙarfafa iliminsu bisa buga lissahin riɓi.
Malami ya gewaya ya duba aikin da ya ba ɗalibbai su yi gida

A ci-gyaran aikin

Malami ya ba ɗalibbai wani aiki su yi bisa ƙananan alluna

| | | |
|---|---|---|
| 3 | 12 | 15 |
| x 2 | x 3 | x 2 |

Ya sake maimaita inda ba su gane ba
Ya ba su aikin yi cikin kayyuna, a ci gyara

| | | |
|---|---|---|
| 14 | 10 | 235 |
| x 5 | x 3 | x 3 |

Ya gewaya ya duba ya ci-gyara a babban allo
ɗalibin da bai gamo ba ya ɗauki gyararren aikin

# DARASI NA 32

Riɓi mai ajiya mai lamba 3 ko 4 ga riɓinyau, 2 ga mariɓinyi.

Tilawa malami ya bi hanyoyi da ya saba don tahiyar da tilawa.

Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su iya buga lissahin riɓinyawa da mayyan lambobi.

Yadda malami zai tahiyar da aiki
Malami ya aza misalin lissahi a babban allo.

$$\begin{array}{r} 327 \\ \times\ 25 \\ \hline \end{array}$$

ya tambayi wanda zai iya buga lissahi ya zo a babban allo, ya buga malami ya ci-gyara.
Ya shaida masu gurin aiki : riɓi mai ajiya mai mayyan lambobi
Malami ya nuna masu yadda ake buga lissahi dalla-dalla.

| d | | g | d.l |
|---|---|---|---|
| | 3 | 2 | 7 |
| x | | 2 | 5 |
| 1 | 6 | 3 | 5 |
| 6 | 5 | 4 | |
| 8 | 1 | 7 | 5 |

-Malami ya bi hanyoyin da ya saba bi don tahiyar da sauran aikin.

# DARASI NA 33

Karatu da rubutun miliyan

Tilawa: bisa aiki jiya

Sabon aiki

Guri : koyon karatu da rubutun miliyan (1.000.000)
Malami ya bi hanyoyin da ya bi ya koya masu karatu da rubutun ɗaruruwan dubbai

Ya ba su misali kamar haka:

$$
\begin{array}{r}
999.999 \\
\times \quad\quad 1 \\
\hline
1.000.000
\end{array}
$$

Ya cika gidajen lambobin

| Miliyan | ɗaruruwa dubbai | Gomomi dubbai | dubbai | ɗaruruwa | gomomi | Diyan lissahi |
|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 0 | 0 | 0 | 0 | 0 | 0 |
| 2 | 0 | 0 | 0 | 0 | 0 | 0 |

Ya sa su rubuta lambar miliyan bisa allunansu
Malami ya nuna masu cewa cikin miliyan lamba baƙwai in an ƙilga kenan gidajen baƙwai ne
Ya tura ɗalibbai su cika gidajen lambobin kamar yanda ya bada
Misali : Ya ci-gyara in sun yi kuskure
Ya ba su aiki ya ce su cika gidajen lambobi a gida cikin kayyunansu.

# DARASI NA 34

Aiki bisa miliyan

Tilawa: bisa aiki jiya

Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su ƙware wajen buga lissahin miliyan da sa shi cikin gidajen lambobi
Malami ya zana gidajen lambobi a babban allo kamar haka:

| | | | |
|---|---|---|---|
| 1.000.000 | 2.000.000 | 3.000.000 | 4.000.000 |
| 5.000.000 | 6.000.000 | 7.000.000 | 8.000.000 |

| Miliyan | ɗaruruwa dubbai | Gomomi dubbai | dubbai | ɗaruruwa | gomomi | Diyan lissahi |
|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 0 | 0 | 0 | 0 | 0 | 0 |

Malami ya yi masu shibtar lambobi
Ya gewaya layi-layi don ya ci-gyaran wanda bai gamo ba
Ya sa su gyara
Sa'annan ya tura ɗalibbai da guda guda su cika gidajen lambobi
Su ci-gyara in sun yi kuskure
Su ɗauki cikin kayyunansu.

# DARASI NA 35

Rabawa marar ajiya

Tilawa malami ya maimaita aikin baya.

Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su iya buga lissahin rabawa marar ajiya.

Yadda malami zai tahiyar da aiki
Malami ya bada misalin : da ya dace don hiddo gurin aiki

Misali : Likita ya raba mutun 4 ƙwayoyin magani masassara 8. nawa kowane ya samu?
ɗalibbai su bada amsa
malami ya gaya masu gurin aikinshi ; rabawa marar ajiya
ya tambayi ɗalibin da zai iya nuga lissahi a babban allo, ya zo ya buga malami ya ci-gyara.
Ya nuna masu dalla-dalla yadda ake buga lissahi.

Ya ba su aikin yi bisa babban allo

```
  8 | 4
    |----
- 8 |  2
----|
  0 |
```

Ya ba ɗalibbai 2 ko 3 aiki su yi a baban allo da guda, ana yi ana cin gyara.

```
4 | 4        6 | 3        5 | 5
  |----        |----        |----
```

Ya ba su aikin yi a ƙananan alluna, ya zanki yi yana gewayawa.

```
2 | 2        4 | 2        8 | 8
  |----        |----        |----
```

A ƙarshe ya nuna masu aikin rabawa marar ajiya mai saura

```
7 | 5        9 | 8        8 | 7
  |----        |----        |----
```

ya ba da aikin yi a gida.

# DARASI NA 36

Rabawa marar ajiya mai lamba 2 ga wanda aka raba 1ga marabai

1.Tilawa malami ya yi hanyoyi da saba don ci-gyara aikin gida.

2.Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su iya buga lissahin rabawa marar ajiya
Yadda malami zai tahiyar da aiki
Malami ya bada misali:

Malami ya bada misali:

Misali : Likita ya raba mutun 9 ƙwayoyin magani masassara 43. nawa kowane ya samu?
ɗalibbai su bada amsa
malami ya gaya masu gurin aikinshi ; rabawa marar ajiya
ya tambayi ɗalibin da zai iya nuga lissahi a babban allo, ya zo ya buga malami ya ci-gyara.
Ya nuna masu dalla-dalla yadda ake buga lissahi.

Ya ba su aikin yi bisa babban allo

| | |
|---|---|
| 43 | 9 |
| 36 | 4 |
| 7 | |

Malami ya bi hanyoyin da ya saba don tahiyar da sauran aiki.

Malami ya ba su aikin yi a gida.

# DARASI NA 37

Rabawa mai ajiya mai lamba 2 ga wanda aka raba 2ga marabi

Tilawa malami ya yi hanyoyi da saba don ci-gyara aikin gida.

Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su iya buga lissahin rabawa mai ajiya mai lamba 2 ga wanda aka raba 2ga marabi
Yadda malami zai tahiyar da aiki
Malami ya bada misali:

Malami ya bada misali: don hiddo gurin aiki

Misali malami gona ya kawo tiya 97 na zaɓaɓɓen iri wake ya raba ma mata 48.Tiya nawa kowane macce ta samu?

```
97 _48__
48   2
 1
```

Malami ya bi hanyoyin da ya saba don tahiyar da sauran aiki.

Malami ya ba su aikin yi a gida.

# DARASI NA 38

Rabawa mai ajiya mai lamba 3 ga wanda aka raba 2 ga marabi

Tilawa malami ya yi hanyoyi da saba don ci-gyara aikin da ya ba ɗalibbai su yi a gida.

Sabon aiki

Guri : ɗalibbai su iya buga lissahin rabawa mai ajiya.

Malami ya bada misali: kamar haka

Malami ya bada misali:

Kungiyar manoman Jaja sun sayi irin wake buhu 279. da damana ta faɗi, an raba ma manomi 25 waɗannan buhunan. buhu nawa kowane ya samu?
ɗalibbai su bada amsa
wani ɗalibi ya je ya buga lissahi.

279 | 25
- 2 | 11
29
- 25
4

Malami ya bi hanyoyin da ya saba don tahiyar da sauran aiki.

Malami ya ba su aikin yi a gida.

836 | 23

998 | 45

514 | 15

# DARASI NA 39

Babbar tilawa.

Malami ya zana masu gidajen lambobi

| Miliyan | ɗaruruwa dubbai | Gomomi dubbai | dubbai | ɗaruruwa | gomomi | Diyan lissahi |
|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | | |

Su cika da lambobi kamar waɗannan : 15, 327, 1245, 23645, 761, 802, 5.966.415

```
  254          375          175        998 | 45
+ 188        - 207        x  25            |
```

Tiyar hatsi guda kilo nawa na ?
ƙwalin sukari kilo nawa ne ?
buhun gishiri kilo nawa ne ?
km metir nawa ne ?

In ɗalibbai ba su gane ba malami ya ƙara ba su waɗansu aiki don ya tabbbatar sun gane.
Ya kuma ci gaba da ba su dogon lissahin kama yadda aka buga su cikin litattafansu.